Jitayi tana San ganin Ya Usman 'dinta da Rukayya da Innah

Tasan da bata xoba ba.
da YUSUF bai hango soyayyar da takema KAMAL 'dinba.
Sagna CE takatse mata tuninta tawajan cemata aunty LABEEBAH kitashi muyi hira dan Allah karkiyi bacci.
Lumshe idanta tayi dan nuna alamun tayi bacci adole
Ganin tayi shuru Sumayya Tace tayi bacci ai
Aikowa cewar Sagna

KAMAL ne yashigo Yana cewa ina suke.
Safna tace Aunty LABEEBAH da Sumayya. Yace eh
Sagna Tace Aunty LABEEBAH tayi bacci Sumayya ko tashiga toilet
Yace OK in tatashi kuce musu mumun tafi gobe kwa rakusu Safna Tace toh yayah saida safe
Yace Allah tashemu lpy ya ficce

LABEEBAH taqara gimshe ido tana shaqar qamshin KAMAL
Ahaka bacci yayi awan Gaba da ita
Cikin caccin natane taji wayanta tana qara taduba taga ba Suna
Tsarin number yasata xubama wayar ido.....
Ya YUSUF ne Yace inbashi number-ki. Sagna ta katse mata tunaninta da fa'din hakan
Waro ido LABEEBAH tayi ta kalleta. Tako gya'da mata kai alamun tabbatarwa.
Tace ok ya naganki ke 'daya. Tace Safna sunyi gun Momy itada Sumayya.. Tace OK
Kara wayan tayi akunnanta da sallama gabanta na fa'duwa dan ba qaramin tsoran shi YUSUF 'din tajiba
Dai-dai nan Sagna tafita
Kamilalliyar muryarshi CE ta isar da sakwanta akunnan nata
Yace meya saki kuka bayan nagoge na'daxo
Tace nifa banyi kuka bah.

YUSUF ya lumshe ido tare da gyara kunciyarsa kallo 'daya xakamai kagano farincin da yake ciki awannan lokacin
Idan kuma kaqarema fuskarsa kallo kagano kishi da rikici kala kala a kwayar idansa

Yace 'daxo mexai kaiki gun Ya KAMAL.
LABEEBAH ta 6ata fuska kamar Yana gabanta Cikin shagwa6a Tace nifah gun XARAH xanje ba gunshi bah
Shuru yayi mata kamar ya sauka akan wayar
Har ta dubah koya kashene sai taga sa6anin haka
Shurun itama tayi tana jiran cewarshi
Ke da waye a 'dakin. Ya jefu mata tambayar
Taqarema 'dakin kallo tace ni 'dayace
Kashe wayan yayi yayinda tabi wayan da kallo tana tunanin shikuma wannan wane irin mutum ne.......
Bata ankareba takai kallantw 'kofah aiko saita ganshi a kofar 'dakin

Gabanta yafa'di
Yace naxone na miki saida safe tunda ke baki iyabah
Taturo baki Tace toh saida safam
Ya harareta Yace mutashi Ipy Yana fa'din haka ya 6acema ganinta
Zuciyarsa cike dajin da'di dama yaxone kawai dan yaqara ganinta dan xuciyar tashice ta buqaci hakan

Ita ko Sam bata samu bacci yanda ya kamata ba dan xuciyar tata da fargaban YUSUF takwana

Washe gari bayan gari yayi haske Su Sagna sukayi skull
Dadynsu ya fitta
Yarage daga Momy sai Su LABEEBAH da YUSUF
Momy takalli LABEEBAH Cikin so da qauna Tace kuje kuyi breakfast mana ranah nayi
Tace toh
Nan sukayi dining ita da Sumayya suka cika cikinsu. Bayan sun dawo falanne YUSUF ya fitoh idanshi ya sauka akan LABEEBAH da take kusa da Momy
Gabanta yafa'di
Yace gudMrning my mom Tace Mrning my son da fatan katashi lafiya
Yace lafiya lau
Sumayya CE tafara gaisheshi kana LABEEBAH
Ya amsa Cikin kulawa kan yajah bakinsa yayi shuru
Ga mamakinsu sai ganin Momy sukayi taje dining ta ha'da mishi breakfast takawo mishi
Sanda ya bafara ci Yace tnx my mom Allah yabarni dake
Tace AmEEn my son
Bayan taxaunane takira darebansu Safna a waya Tace inasan xuwa anjima kakaimin wasu yarana gidan KAMAL. Yace toh ranki yada'de. Takashe wayan idanta akan YUSUF
Yace mexai hana insun gama in kaisu dan Xanyi tagun
Tace Yauwa mah

Sha biyu saura suka gama shirinsu tsaf tare da yima Momy sallama
Tace kwana biyu xaku mata fah. kodawo Ku qarashemin kwanakin naku
LABEEBAH tayi Murmushi Tace toh Momy
Sumayya Tace Su Sagna xasu xoko
Momy Tace eh kai xaku gansu
YUSUF Yace toh muje
Nan suka shiga motartashi duk kansu agidan baya suka xauna
Haka yajasu Sumayya nata xubah YUSUF na'dan biye mata
LABEEBAH dai binta take da eh ko aa
Yana yin fakin suka fara ciki kicin bu'de kofar Amma taqi bu'duwa
Fitowa yayi ya bu'dema Sumayya tafitoh Yace Auntyn naki xata rakani anguwa.
Sumayya tayi Murmushi Tace toh sai kundawo
Yace Yauwa qanwata Aunty XARAH

Tace toh
LABEEBAH najin haka tafitoh da sauri Tace niba inda xan rakaka. Tafa'di hakan da niyar bin Sumayya Cikin gidan

Ganin haka yasa yayi saurin riqo hannunta da sauri Sannan ya 'dagama Sumayya hannu alamun saisun dawo ta gya'da mishi kai.

🌵🌵🌹🌹🌵🌵
*MASEEFAR SOO*
🌵🌵🌹🌹🌵🌵

Sanda ya tabbatar da shigan Sumayya gidan Sannan ya kalli LABEEBAH da wani mugun kallo tare da sake mata hannunta ya bu'de mata gidan gaba cikin 'daure fuska Yace shiga mu tafi Cikin tsoro tashiga kamar tarushe da kuka. Sannan shima ya shiga yajah motar

Awani gun shaqatawa yayi parking

Asan nanne ya kalleta Yace saboda kina xumu'din San ganin Ya KAMAL shine yasaki qin San binah

Ta kalleshi ka'dan Tace ni bashi nakesan gani ba

Yace maqaryacciya abin nan naban mamaki. Akanme xaki SOO Ya KAMAL Yana mijin 'Yar uwarki

Nima ban sani ba. Tabashi amsa cikin jin haushi

Yace dokokin daxan dinga miki shine

Wlhi naga ko da wasa kin kalli Ya KAMAL saina mugun 6ata miki Wlhi

Ke barima kiji namiki gwari-gwari daga yau banaso naqara ganinki da shi. Ko hanya ce taha'daku toh kicanja hanya. Sam karna kuskura naga kinyi sanadin daxaku ha'du da juna Inba hakaba saina gayama XARAH cin amanar da kika mata nasan mijinta

Kuka LABEEBAH tafashe dashi mecin rai tayi da nasanin xuwa Abuja

Imin shuru kafin in maqureki anan

Shuru tayi

Yaci gaba da cewa dafatan kinji me nace miki

Cikin shagwa6a Tace naji

Yace gud my baby toh share hawayan ko banasan kukan.

Jitayi kamar ta sheqa mishi mari dan takaicinsa

Ya sata kuka kuma ya lallasheta

Saka bayan hannunta tayi tana goge hawayan

Ganin haka yasashi janyota jikinsa ya ha'data da qerjinsa Yana goge mata da hankicif 'dinsa ahankali

Itako lumshe ido tayi danjin da'din turaransa

Yace am sorry babyna xaki sha ice-cream

Ta'daga mai kai tayi ahankali

Yace. Toh bari na kar6o miki ko. Yafa'da yana me xareta daga jikinsa
Sannan ya fitta daga motar
Shuru LABEEBAH tayi tana tunanin shi
Tana kallo ya siyi biyu nashi da nata.
Ya shigo motar ahankali ya rufe tare da kallanta.
Ya gyara xamansa sosai yana fuskantarta. Tare da bu'de ice-cream 'din Yace toh bu'de bakinki
Ta kalleshi qasa qasa Tace xansha da kaina
Yace no nusuwata bu'de in baki. Taturo baki Tace nifah da Kaina xansha
Wani kallo yajefeta dashi. Bashiri ta bu'de bakinta yabata

Haka ya dinga bata tana Sha ha'de da lumshe ido dan da'di

Gareshi ko hakan ya fara jefashi cikin wani hali
Dan haka ya fara bata da sauri
Sanda takusa shanyewa tace ta'koshi
Bai matsa mataba yabu'de nashi yasaka mata kan cinyarta yace na baki dan haka nima saiki ban

Tawaro ido Tace banta6a bah atututan mutum abu bah

Yayi Murmushi Yace habah nutsuwata nine qatu. Yafa'da shima da waro idon
Tagya'da mishi kai alamun tabbaci
Yace bani dan Allah
Ta kalleshi ka'dan xatayi magana ya 'dan harareta

Murmushi tayi tafara bashi ahankali ahankali. Duk lokacin da xata bashi saiya wurga mata kallan SOO. Saitaji wani iri

Sam bata gane bah dan damuwarta shine yakaita gun XARAH. Ahaka dai yasha da'dan dama. Kana kallansu kaga masoya a xahiri Amma a ba'dili LABEEBAH batasan hakaba hasalima dagaske 'daxu xumu'din San ganin KAMAL 'dinne yaso hanata binsa kamar ya fa'di

Yauwa nutsuwata yanxu muje innuna miki garin abujah kafin mukoma ko

Tace toh dan Wlhi tsoran shine yake shigarta. Dan batajin xata iya mishi musu akan Komai

Haka YUSUF ya dinga yawo da ita yana jin da'di

Tabbas garin abujah ta ha'du iyakar ha'duwa hakan ne yasa LABEEBAH sakewa dan tanasan rayuwar yawo. Musamman tawannan tabu'de ido

Sun biya ta supermarket yasiya mata kayan xaqi da sauransu

Ahan yar Su tada wowane tana shan sweet Yana kallanta cikin SOO da kauna.
Yace nutsuwata
Takalleshi Tace meyasa kake kirana da hakan. Yace haka kawai dan kindace da sunanne.
Shuru tayi
Shima shurun yayi........
Ta dubah wayanta ga mamakinta taganta akashe Tace la wayata tamutu bayan acike take da chaji. Tafa'da tana me kunna wayan. Sai taga ta kawo
Yace nina kasheta
Tace meyasa
Kai tsaye Yace saboda banasan XARAH da Ya KAMAL Su damemu

Tace Amma hakan yadace dan hankalinsu sai tashi kuma Wlhi inasan ganin........

Ya KAMAL
Ya katseta da fa'din hakan
Kobashi kikesan gani bah
Cikin wani yanayi Tace XARAH nakesan cewa fah
Yace gud niba qaramin yaro bane
Tace Wlhi XARAH xance......
Tsayawa yayi da motar agefan titin ya fuskanceta sosai Yace baxa kiga XARAH da Ya KAMAL bah. Dan yanxu haka gidan Momy xan maidake
Afurgice takalle shi tare dayin larai-larai da ido. Hawaye nasan xubowa
Ya gallah mata harara Yace Wlhi kika sake hawayannan ya xubu saina tsinkeki da mari.
Aituni tamai dashi tana 'kifta ido
Yajah qarimin tsaki dajan motar. Haka motar ta'dau shuru har suka iso gidan Momy xata fitta ne
Yace kinga malama ban sallameki bah
Bata kalle shibah Amma tafasa ficewar
Yace idan Momy tatambayeki yasu XARAH kinuna mata kamar acan kika ini
Sannan idan XARAH takiraki kikawomin wayar ninasan abinda xan gaya mata.
kinji nutsuwata. Yaqarashe da lallashi

Tattaro jarumta LABEEBAH tayi tagallah masa harara Tace idan naqifah.
Yayi Murmushi Yace xaneki xanyi
Tace sai kace wata 'dalibarka
Yace lah😳
Aike yanxu kinxama 'yar rainona kinga bana saki asahun la'dibai naba
Dan kinsan shi 'dalibi malami yakan 'dan rangwanta masa. Amma 'yar raino bata buqatar rangunci
Ta kawar da kallanta daga kansa Tace kai xaka gane wannan karatun naka koko ince xauranci
Ya 'dan janyota jikinsa da muryar lallashi Yace kwarai da gaske Amma dan Allah kiyi abinda Nace miki plx kitemaken
Qara langwa6emai tayi tare da 'dago fuskarta xuwa kallansa  Tace  nima katemaken naga XARAH
Yace namiki alqawarin gobe xaki ganta da yardar Allah
Tace ko
Cikin marairaice mata Yace  Allah da gaske
Yafa'da daniyar kai mata kiss 💋A mma ya fasa........
Xatayi magana kenan   kiran wayan KAMAL ya shigo. takalli YUSUF ka'dan a'dan tsorace...

Da shagwa6a Tace Ya KAMAL ne in 'dauka
Cije le6e YUSUF yayi tare da qara maqaleta. ya kai bakinsa kunnanta Yace banaso ki'dauka Amma tunda kinaso 'dauka

Aiko da sauri ta'dauka tare dasan raba jikinta da nashi Amma yaqi yarda da hakan
Yaqara maqaleta
Tace hello Ya KAMAL................
Wani burkitaccen kiss YUSUF yakai mata awiya me shiga cikin jikin mutum batare da ya ankareba
Ai LABEEBAH batasan lokacin da tasaki wayan Tafa'di a gefanta bai. batir 'din ya fita
Mai makwan tabi wayan saita kwantar da kanta a qirjin YUSUF tabi wayan da kallo
shiko YUSUF abinda yake so kenan dan haka ya 'dago ha6arta
Yace yadai taturo baki kallo 'daya xaka mata kasan jikinta ya mutu. Da shagwa6a Tace wayan tafa'di
Cikin kwai kwayan Muryarta Yace toh me kikeso namiki
Tace nidai kakira min shi naji mexaice
Yace wlhi baxan iyaba nutsuwata
Saita fashemai da kuka tana cewa nidai gaskiya kakira shi
Shuru YUSUF yayi
Can Yace kinasan na kira miki shi ko
Ta'dagamai kai
Yace toh kibari anjima saina kira miki shi
Tace nidai.......
Ya katse da cewa xakiyi biyu babu in Kika matsamin
Shuru tayi
Shima shuru yayi

🌵🌵🌹🌹🌵🌵
*MASEEFAR SOO*🌹
🌵🌵🌹🌹🌵🌵

Sun 'dauki minti biyar 5 ahaka shuru mabai magana. Saima da'da langwa6emai da tayi
Ganin haka yafara shiga wani yanayi yasashi xareta daga jikinsa xaiyi magana kenan suka hango Safna da Sagna sun fitoh
Da kalleshi Tace dan Allah bu'demin Ya YUSUF plx
Saurin goge mata hawaye yayi da hankicif 'dinsa Yace plx kisan me xakice
Murmushi tayi tace kanasan koya min qarya.
Yace kare kanki xakiyi dan sunsan bana duka bare suyi tunanin ko na dakekine kanta tayi magana sun iso
Ya xuge gilashin motar suka leqo da kansu
Sagna Tace lah Aunty LABEEBAH yanxu fah muke shirin xuwa
Ta qaqalo Murmushi Tace eh gashi Ya YUSUF ya dawo dani
Tayi dariya Tace Yauwa gwanda dama kinga saimuyi kitsammu ko
Safna Tace hakane gobe maje
Ya yadanna gefan motar saiga kofar tabu'de da sauri LABEEBAH tafita tana cewa muje inyi Sallah saimu fara ko
Aiko Sagna da Safna suka bi bayanta Suna cewa bakiyi bah
Tace eh Wlhi

YUSUF yashafah kansa tare da sauke ajiyar xuciya dan ganin tamanta da wayarta ya 'dauka yajefa ajjihunsa Yace godiya gareka Allah
Na roqeka karkasa Yayana ya ankare da wannan baiwa taka
Idan Santa alkairine agareni kamallaka min ita
Yana fa'din haka yajuya kan motarsa daniyar yin masallaci.

Momy Tace yana ganki 'Yata
Ta'dan rufe ido cikin kunya Tace hmm inasan xama kusa dake ne Momy
Cikin jin da'di Momy ta rungumeta Tace ayya Nagode sosai 'yata ina tare dake.

LABEEBAH jin sanyi tayi aranta koba Komai tanada Masoya  Innah Ya Usman XARAH Sumayya ga Momy mah. Kuma tana hangen tausayinta a idan KAMAL
Tagode ma Allah daya barta dasu

Haka tayi Sallah tayarfema Sagna da Safna Kansu da kitso Wanda kallo 'daya xakama kannasu kayi tunanin injinne ya xane kan dan tsabar kyau dakan da yayi

7:00pm nayi sai ganin Sumayya da YUSUF LABEEBAH tayi
Sanda suka ke6e Tace ya haka
Tace hmm Aunty LABEEBAH kedai bare Ya YUSUF akwai tsari bansan me yagama Aunty XARAH bah kawai sai cewa yayi inxo mu tafi tace ingaishe mata dake

Tace hmm namanta wayata a motarsa
Sumayya Tace nako ganta agunsa

8:30pm na dare ne Suna hirarsu me da'di a'dakin Momy. Momynma tana 'dakin Dady
YUSUF yashigo Yana cewa nutsuwata
Duk suka sura mishi ido
Sagna CE Tatashi tace Ya YUSUF kayi budurwane Yace me kika gani Tace Naji ka'ambaci nutsuwata ne
Ya saci kallan LABEEBAH tare da ta6e baki Yace share kawai xokiji
Tace toh tabishi
Safna takalli LABEEBAH qasaqasa batadai ce Komai
Sumayya ko taji meyace Amma tunaninta ko waya yagamayi shine yashigo da qarashen Kalmar a bakinsa.

LABEEBAH ko dama tasan da ita yake.......
Sagna CE tashigo da murnarta Tace Aunty LABEEBAH Momy nakira
Da sauri LABEEBAH Tace toh tana ina Tace tanacan falan mu
Toh Tace tafitta

🌵🌹🌵🌹🌵
*MASEEFAR SOO*
🌹🌵🌹🌵🌹

Waige wage  tahauyi dan bata hango kowa bah
Rufffff
Taji an rufe  mata ido ta baya
Tajah numfashi dan tagane waye Tace Ya YUSUF.......
Yace na'am nutsuwata. Yafa'di hakan da xagayowa gabanta
Tace Kaine Momyn Yace eh
Tace toh miye
Yace kafin muxogun ya akayi kika gane nine
Kawar da kanta tayi daga kallan fuskarsa tace qamshinka ne ya ganar dani kai
Yace watoh kenan kinma qamshin turaran Ya KAMAL farin sani
Takalleshi ka'dan. Nan tahango rikici da futuna acikin idan nashi

_ai har duniya tana'de nayima turaran Ya KAMAL farin sani. Eh qamshinsa Yana sani nutsuwa. Tafa'di hakan aranta_

Afiliko cewa tayi aa banta6a riqe qamshin waniba sai naka
Yace gud
Dama kwalliyarki CE tamin kyau shine nakisan 'daukan ki photo
Taqare mishi kallo Tace kayi kyau kaima sosai
Yayi Murmushi Yace aisaimu mu'dauka tare in ba damuwa
Tace mexai kawota
Yace Mene
Tace damuwar
Matsowa yayi kusa da ita suka jera tare da seta wayanshi ya haskesu da hotuna
Haka yadinga 'daukarta Sannan Yace yunwa nakeji nutsuwata
Tace toh kaci abinci man
Ya kalleta da wurga mata mata wani shegen kallo. Wanda yasata sunkuyar da kanta da sauri dan taga irin abinda yake fitowa daga cikin KAMAL Wanda yake shiga idan ta shinetoh yake qoqarin shiga idan nata yanxu
Ya 'dago ha6arta Suna kallan juna Yace plx ki fanshi Momy dan Allah kiciyar dani yanxu
Da'da ware ido tayi Tace meyasa saini

Yaqara kusanta kanshi gareta kamar xai rungumeta Yace saboda natsinci kaina cikin farin ciki 'daxo da kikaban ice-cream plx gobema xaki qaraban. Yaqarashe da shagwa6e mata.
Ba qaramin rikicewa LABEEBAH tayi bah
cikin sauri Tace eh Allah ya kaimu
Murmushi ya sakar mata kana ya'dan nesanta kanshi da ita Yace muje ko
Cikin sanyi Tace xuwa inah
Yace Wlhi indai yanxu mah baki ciyar danibah baxan iya bacci bah kuma baxanci bah
Jan numfashi tayi Tace  gaskiya kana da futuna Ya YUSUF

yayi Murmushi tare da kama hannunta sukayi dining Yana cewa Hakka abinxai kasance in raineki kema Ki rainan

Murmushi itama tayi taha'da mishi abincin 'dan dai-dai
Tamurje idanta dan taga kam shi bah kunyace dashi bah
Ta'dinga bashi Yana xuba mata kalmomi masu kashe jiki
Daqer tasamu kanta agunshi dan biyayi yadinga kananna'deta da hira
Sanda takai shi har kusa da part 'dinsa Sannan Tace saida safe. Harta juya Yakama hannunta yayi mai kiss
Mutashi Ipy nutsuwata.
Xanyi baccin farin ciki yau. Yafa'di hakan da sake mata hannun
Tace ayya nataya murna. Tana fa'din haka tayi tafiyarta yabita da kallan soyayya

Washe gari da kamar qarfe 8:00
LABEEBAH CE da Sagna Suna ninke Kaya
Sumayya da Safna ko Suna kitchen Suna fitoh da breakfast
Momy tashigo 'dakin nasu tace da Sagna ke jeki kiramin yayanku maxa yaci abinci dan jiya baiciba
Tace toh
Momyn tafitta

_LABEEBAH Tace aranta Allah sarki Momy bakisan Ni yasaka agaba na bashi bah_

Sagna takalli LABEEBAH Tace Aunty dake fah Momy take
LABEEBAH Tace kai haba.
Saboda qarya sagna harda cewa Allah
Saka hijab LABEEBAH tayi sannan tayi part dinsa

Ta kwankwasa dayin sallamah
🌹
YUSUF dake xaune Yana rubutu a hannunsa. Ni Rahamat naleqa hannun nasa naga rubutun da yayi kamar haka
*ina sanki labeebah*
Jin muryarta tana sallama ha'de da kwankwasa mai 'kofah shiya sashi saurin tashi da bu'de mata 'kofar
Barka da Safiya momy CE take San ganinka yanxu

Ya harareta Yace wato Momy CE mesan ganina banda ke.
Dan Ya KAMAL ne wanda xakiso ganinsa ko
Xatayi magana kenan idanta ya sauka akan hannunsa ganin yasa *ina sanki LABEEBAH* yasa gabanta fa'duwa lokaci 'daya kuma tayi kamar batagani ba. Ta gyara tsayuwarta tana rayawa

aranta Allah nagodema daka nunamin Hanyar ramuko.
Cikin fusata Yace kin wani yimin shuru kibani amsa mana
Tace dan Allah dakata Malam aisai yanxu nagane xafin sone da kishi suka maka yawa shiyasa ka'isheni da xancan YA KAMAL

Yajafa mata wani shukumin kallo

Ita kuma Ta galla mishi harara

Tsugun nawa yayi agabanta Yace

🌵🌹 *Maseefar soo* 🌵🌹

Akan sanki bana bam bamce da ranah
Akan sanki nakasa bacci
Akan sanki narasa nutsuwata
Akan sanki xan nuna abinda yafi xafin soo da kishi
Har abada xan isheki da xancan YA KAMAL inhar baki hakura sanshi bah

Jikinta LABEEBAH ne ya mutu
Tace abinci xakaci da alama plx tashi kar momy tagaji da jira kuma naga jin yunwa atattare dakai
Yace plx ki kauda yunwa sam bata atsarina. Wlhi kallan hotanki shine abinci na
Dan Allah karkice bakya sonah

Saka hannunta tayi takama nasa hannayan yatashi Tace kaje kiran Momy xuwa anjima kaxo ka'daukeni shan ice-cream
Manna mata kiss yayi agoshi Yace OK
Allah ya kaimu ina zaki ban
Tace sosai mah dan har sai kace ya'isheka

Qarfe biyu ne na ranah
Tana tsaftace jikinta a toilet
Tana tunanin yanxu haka YUSUF Yana Hanyar xuwa sutafi

Sai kuma me 😳

Jitayi mararta ta mur'da mata sosai har takaita ga dur qushewa tana wayyo Allah
Cak kuma ciwan ya 'dauke
Tayi saurin fitta daga toilet 'din hankalinta tashe

Karo sukayi da safna Ta kama hannunta hawaye nasan xuba mata Tace na shiga uku al'adata zataxo plx temakeni
Cikin wani hali Sagna taduro daga kan gado Tace ayya bari........
Momy CE tashigo da wasu Kaya ahannunta ganin LABEEBAH cikin kuka tasaka kayan gefe tare da riqeta Tace meyaru menene Tace Momy al'adatace taxo Momy ina shan wahala sosai Momy
Momy Tace toh wane magani kikesha.......
Wayar Momy tahau qara ganin KAMAL tayi saurin 'dauka Yace plx Momy kikula da LABEEBAH tanada ciwan cikin na qarshen wata kuma yau nake tunanin xuwanshi tun jiya nakira numbarta ban jitaba plx kibata wani abu kafin natawo mata da maganin nata plx Momy banasan yatashi mata hankalina natashi
Tace toh gashima yanasan tashin mata.......

Yace what......
Plx Momy kiyi mata wani dan Allah wlhi banasañ tasha wahala
yanxu mah dan xan shiga wani aiki ne dakin ganni
Amma ina fitowa xanxo Tace toh shikenan ya kashe wayan

Momy ta kamata suyi 'dakinta anan tabata wasu magunguna tasha
Amma me ko cikakken minti biyu batayi da shaba marar taqara murtawa
LABEEBAH tasaki wani qara nan take taxube jikin Momy numfashinta na samaluuuuuu qasaluuuuuu
Agigice Momy tafara kiran sunanta cikin rikicewa Tace nashiga uku ke LABEEBAH karkiyi haka mana.
Cikin wani yanayi Tace Momy cikina xan mutu xan mutu wayyo momy.
Da sauri Momy tace dasu Sumayya kutemaka min mukai mota........
Kan suyi wani yunkuri sai ga YUSUF yashigo da murnarsa........
Aiganin LABEEBAH haka yasashi saurin qarasa shigowa Yace innalillahi mom meyasa meta Tace temakamin mukai aaibiti dan Al....
Aibata qarasaba YUSUF ya sureta sai motah. Momy taxari mayafinta tabi bayansa
Tana shiga ita da Safna yanajan motar kamar xaitashi sama. Xuwa lokacin ko LABEEBAH ta sume....

Direct asibitinsu KAMAL yaje
Momy tambaya take ina KAMAL doctors sukace mata yashiga wani yanxu
Dr Jameel abokin KAMAL shi ya dubata
Yaba kulawar da tadace sosai
Kana shida YUSUF suka xuba mata ido
Shidai Jameel tuninsa biyu ne
nafarko dama LABEEBAH tana nan garin Abujah ne shiyasa dayaje kano shekaran jiya akace mai batanan
Kuma dama danada irin wannan matsalar me tada hankalin Masoyi

Lalle dole yanxu ya shige mata koya sami kanta ta'amince mishi da Auran ta🌹

Shiko YUSUF duk da a labarin da XARAH tabashi na LABEEBAN na ciwan nata. Baiyi tunanin yana bata wahala hakaba.
Lalle dole ya Aureta cikin lokaci qanqani dan baxai gure ganinta haka bah.
Jameel ya kalli YUSUF Yace bari na'danje in duba wata ina xuwa
daqer YUSUF ya iya cemai toh sannan ya bishi da mugun kallo dan sai yanxu ya tuna Ashe shima yana San LABEEBAH.
Mtww..... Yajah tsaki Yana cewa aransa yayi takaicin qin xama doctor dabaiyiba da bawanda xai ta6a mishi LABEEBAH sai shi
hmmmm
( *YUSUF DA KISHI*)

Momyce tashigo itada Safna kallo 'daya xaka musu kagane basa cikin nutsuwarsu
Ta kalli YUSUF Tace Yace ya 'dorata akan wasu allurai qila tafarfar'do anjima Ko cikin dare
Yace toh Allah yasa
Sagna tace AmEEn
Sun 'dauki lokaci ahaka kowa da abinda yake kissimawa aransa
Can YUSUF Yace toh Momy bari inje duba wasu Kaya da aka kawo mana zuwa anjima xan dawo Tace toh
Tare suka fitta
su Momy suka xauba nan wani extra 'dakin da makusantan mara lafiya da suke xama

🌵🌵🌹🌹🌵🌵
*maseefar soo*🌹
🌵🌵🌹🌹🌵🌵

Aiki KAMAL kawai yake Amma hankalinsa nakan LABEEBAH Sam xuciyarsa takasa nutsuwa
Na Musam man gaban shi yake fa'duwa idan yatuna mafarkin da yayi da ita jiya.
Ya ganta tanata kuka Sannan shi Yana kanta Yana kallanta yanajin xanfin kukan nata Amma haka yabarta tana kukan batare da yayi yun 'kurin hanata kukan bah

Cire safar hannunsa yayi ya saka gyefe Yana hamdala ga Allah daya bashi sa'a akan aikin
Yakalli Dr yaxeed Yace nagama nawa saura naku
Dr Aryan Yace Bayan kagama Komai
Yayi Murmushi Yace kuma fah. Ya fa'di hakan Yana mai ficcewa

Kamar ance kalli can....
Ya hango YUSUF ya ficce daga asibitin nasu can kuma yaga Momy da Safna sunyi jigun jigun Gabansa ya fa'di abayyane Yace shikenan ta sume 😒
Cikin damuwa yanufi gun Momy Amma Jameel ya dafashi Yana cewa habah abokina dama Masoyiyata tana cikin irin wannan halin kakasa fa'damin

Yace am sorry bamu samu zamah bane.
Yace OK tana part 'dina xaka ganta acan
Yace ba matsala.

Fasa bi yayi takan Su Momy yayi gun LABEEBAH.
Ahankali ya bu'de kofar yamayar ya rufe
Idan shi ya sauka akan fuskarta nan take yaqara ware idan nashi ganin tayi mishi kyau haskenta yaqara fitowa Amma har miyanta ya'dan fa'da.

Ya janyo kujera ahankali yaxauna idanshi dai Yana kan fuskartata.
Yasa hannunsa kan goshinta xiiirrrr na wani shock yaji
daga ita har shi dan ita furgita tayima Amma ba a hayyaci bah.......
Cikin wata wahalalliyar murya wanda duk me sauraro indan yajita yasan ba'acinkin hayyaci aka fa'detaba.

Tace
KAMAL.......
Idanta arufe dan idan da xata farfa'do ace mata ta'ambaci Kalmar KAMAL cewa xatayi qarya ake mata

KAMAL...... KAMAL...... KAMAL......

KAMAL ya maimaita sunan data ambata. Har so uku
Kwakwalwar shice ta muntsine shi tare dayi mishi wani suddabaro Wanda yasashi Agigicewa ya kuma tashi a gigican tare waro😳 ido
Yace plx Laveevah plx
Karkimin haka plx
Ya fa'di hakan Yana ja da baya da baya Tare da dafe kansa.

Me yasa kikamin haka
Me yasa sai yanxu xaki bai Yana agareni
Meyasa meyasa meyasa. Kamar da KAMAL yaketa furtawa kenan.
Kallo "daya xakamai kasan xahiri Yana cikin tashin hankali
Ahakan yafitta daga 'dakin. Direct motar shi yashiga ya figeta da gudu kamar me gudun

mutuwa karta kamashi
Doctors dasu Nurse da ma'aikatan gun sukabi motar da kallo Suna tunanin anya lafiyan Dr KAMAL kowa.

Momy ko kasa jurar xaman tayi. Nan takoma gun LABEEBAH taxauna kawai tana kallanta dayi mata addu'ar Allah yabata lafiya
Safna Tace Momy jiba.
Har wiyanta yafah
Cikin tausayawa Tace eh ko. Gashiman
Ai tana kar6ar jarabawa Allah yasa kicinye
AmEEn Safna Tace

Qarfe 8:00pm dai-dai YUSUF yakoma asibitin
Nan yatarar da Momy dasu Sumayya harda XARAH
Yace har yanxu bata farfa'doba. Momy Tace tukunma dai
Ya shafa kansa cikin damuwa
Momy takalleshi Tace banga Yayanka bah
XARAH Tace Yana gida Momy alamu sunmuna bayajin da'di. Sannan na tambaye shi Yace Bakomai
Tace ban sanshi da riqe abuba.
dama wannanne.......
Tanuna YUSUF
Toda nace akwai abinda yake damunshi
Amma tunda kikaji yace haka toh bashakka ba Komai ne

Shidai YUSUF xubama LABEEBAH ido kawai yayi
Yana jin dama ciwan yadawo kansa

Anan Sagna da Safna da Sumayya suka kwana

Kusan qarfe 1:00pm na ranah LABEEBAH tafarka
Lokacin YUSUF ne a'dakin dan haka yayi saurin matsawa kusa da ita
Yace aminci ya tabbata ga sarki Allah daya tashi kafa'dar masoyiyata
Dafatan kin samu kanki lafiya kuma ina addu'ar Allah yasa bawani sauran ciwo da yayi saura agareki
Idanma akwai naro'ke ka Allah kadawo dashi kaina.

Murmushi tasaqar mai Cikin sanyi Tace Nagode da kulawarka gareni
Ina maka fatan alkairi
Ya ta6a goshinta yace NI DA KE
Tace xanso ganin XARAH Yace yanxuko suka fitta sallah.
Tace ayya
Yace ina fatan ba inda kuma yake miki ciwo.

Tace ba ko ina danma jina nake garau
Yace gud godiya ga Allah mahalicci
Tace inasan tsaftace bakina
Yace toh gyara in kaiki toilet
Saurin miqewa tayi da harararsa Tace da dafata da vasai kakaini ba
Kidaibi ahankali dan karki jamin....

Murmushi tayi kawai tayi toilet
Nan taga Komai sabo dan haka ta tsaf tace bakinta ha'de da gabanta Sannan tafitoh taxauna gefan gadon tana cewa yunwa Ya YUSUF

Ha'da mata abinci yayi ya koma gefan gadan kusa da ita Yace gyara in baki ko
Tako matsa kusa dashi yadinga bata tana ci Yana gaya mata da'da'dan kalmomi
Sanda takoshi Tace toh nima bara in baka
Yace kamarko kinsan yanxu nasaba da ciyarwarki
.
Tawaro ido Tace so 'daya ne fah
Yace eh 'dayan fah
Dan duk sanda naga abinci ke nake tunawa
Daidai nan tagama xuba yanda take tunanin xai iya ci Tace hmm ha
Ya bu'de bakinsa tadinga bashi itama
Kallo 'daya xaka musu subaka sha'awa

Sanda suka gama budirinsu Su Momy suka shigo
Nanko suka cika da murna ganinta Tatashi
Momy Tace yanxu sai muyi gida ko
Cikin sanyi XARAH Tace dan Allah Momy tayi gidana ko kwana 'daya ne tayi plx

YUSUF Yace habah dai waike dolene saitaje gidanki kibarta gidan Momy mana
LABEEBAH ta kalleshi nan tagano mutuminshi na yawo afuskar tashi Wato kishi

XARAH ta harareshi Tace kabini ahankali ko in wargaxa maka shiri wajan lemo KAMAL
Atare LABEEBAH da shi suka kalleta
Yace kai habah ai Yana tare da ita saidai yanxu tajuya masa baya

Tace waya gayama yananan daram bana tunanin xata juyamai baya

Ya kalli ABEEBAH da galla mata harara tare da cewa kice wani abu man.....
Tayi saurin kallan XARAH dace mata waya gayamiki
ai nada'de da rufe shafinsa araina
XARAH Tace story kenan
Kicire tsoran YUSUF kifa'di gaskiya
Cikin fusata YUSUF ya harareta Yace Allah xamu 6ata

Tace inmun 6ata xamu shirya Amma kasani yau ranatace

Momy tayi Murmushi Tace Ku kuka San xaurancanku
Yanxu dai kai YUSUF ka'dauki LABEEBAN da XARAH kakaisu gidan nata

Mu kuma mah tafi a motar Sagna

Bayanda YUSUF xaiyi haka yabi umarnin Momy yayi gidan KAMAL dasu. Xuciyarshi namishi xafi ha'de da jin haushin XARAH dan bayasan ha'duwar LABEEBAH da KAMAL sam

Daga faking 'din da yayi xaka gane ran maxa a6ace yake
XARAH tafitoh Tace 'dan saurayi karka fashe nabaka minti biyu kafin kashigomin da ita
Idan kawucce xanxo in 'dauketa inga tatsiya
Ya gallah mata harara. Itako tashige ciki abinta
Ga mamakinsa saiji yayi LABEEBAH takamo fuskarsa da hannu biyu

Tana kallansa Tace kwantar da hankalinka My  SUP
Karkasa wani damuwa aranka bare ya baiyana cikin kwayar idanka. Kabani minti biyu kacal👌 xanyi wanka in fitoh muje shan ice-cream
Manna mata kis yayi agoshi Yace Yauwa nutsuwata plx Karki wacce haka
Tace toh taso muje
Yace ina jiranki anan Tace toh tafitta daga motar tayi ciki

Wow Tace ganin yanda falan ya qayatu da kayan alatu Tace gaskiya ne........
Kamar ance kallican....
Taga wani kyakkyawan hotan XARAH da KAMAL
Ta'isa gun hotan da kyau. Tatsaya tana kallah
Xakayi tunanin XARAH take kallo nan ko KAMAL taxubama ido.
Xuciyata namata da'di da ganinsa.....
Motsi taji abayanta dan haka tajuya ahankali.
XARAH tagani Tace munyi  kyauko
Tace sosaima da kubani
Tace ainaki na musam man ya miki ni dake da shi
Tace abin xaibada armashi
Saima kingani.  cewar XARAH

Tace Wanka yanxu dai Xanyi dan Ya YUSUF na jirana
Tace watoh dai baxai barkiba
Ai anan Xan kwana nagadai plx kidena takurama masoyina
XARAH Tace .kai habah yaushe KAMAL yafitta daga ranki
Ai KAMAL bsxai ta6a fitta daga rainaba saidai ko ya baiyana agareni YUSUF xan Aura......
Dalili...
XARAH takatseta da fa'din hakan

Plx kinunamin toilet dan Allah
Tace ai'daki na musamman na ware miki gashican
Da Murmushi LABEEBAH tanufi 'dakin.
Direct toilet tayi. Tayo wanka da sauri sauri tafi toh
Nan taga wasu Kaya da XARAH ta ajiye mata
Duguwar riga da takalmi me tudu da wani qaramin jiyabi gayu
Ta'dauka tasaka. Nan tafitoh kamar sarauniya
Sin full make-up tayi da feshe jikinta da turare
Tasaka takalmin  dasaka hijabi gayun

XARAH tashigo tana cewa kinyi kyau sosai
Tace nagode bari inje Yana jirana
Tace toh
Nan tafitta

Yana jikin motar hannunshi har'de da juna Yace wow nutsuwata tawo ahankali in baxaki iyaba na 'dakeki
Tace hmm xan iya. Taqarasa gareshi yabu'de mata motar tashiga yarufe
Sannan shima yashiga yajah motar........

Da gaske wajan shaqatawa sukayi abinda yaba LABEEBAH mamaki shine ganin ba inda sukaje ranar bane wani gune daban.
Yasiya musu ice-cream 'din Yace gashi gareki taurarwata
Tace ta yanxu nixan fara baka
Yace no in nafara baki aiba wani abu bane Tace toh fara ban Yace OK
Nan yafara bata tana Sha tana lumshe ido
Jama'a da dama Suna binsu da kallo lokaci lokaci cikin sha'awarsu

Daya gama bata sai tabashi yasha San ransa

Suka tashi suka 'dan xaga gun cikin jin 'dadi da farin ciki
Kana suka dawo motarsu da barin gun

Biotic yakaita Yace muje ciki ki'dauka abinda kikeso
Tace kai Ya SUP ya kashe mata ido 'daya Yace menayi Tace Bakomai
Yace toh muje
Haka suka shiga taga qananun Kaya kamar banxa. takasa 'daukar Komai. Ganin haka ya dinga jidar mata dogayan riguna Yana cewa dasu kika dace
Itadai binshi da kallo kawai take haryagama Sannan ya kalleta Yace nagama nawa saiki xa6arma XARAN Ki da Sumayya Tace toh
Nan taxa6ama XARAH masu kyau da Sumayya
Sannan taga yabada ATM 'dinsa aka cire ku'din Wanda tasan ba qaramin ku'di bane
Sannan suka fito da Kaya niqi niqi

Sai godiya take masa

Da yayi faking a gidan XARAH Yace plx nutsuwata Ki kulamin da kanki
Tace insha Allah
Yajah qaramin tsaki dacewa plx muje gidan Momy Wlhi hankalina yakasa nutsuwa da kwananki anan.
Tajah numfashi Tace mekake tsuro ne MeeNi
Kai tsaye Yace ha'duwarki da Ya KAMAL
Tace tab ina tabbatar maka har nakwana natashi baxan yarda mu ha'du bah. Banfah manta da kashedin da kaminba
Yayi Murmushi yace Allah ya barni da ke
Tace AmEEn
Xata futa ya kama hannunta ya sumbata Yace kiyi mafarkina kinji Tace toh
Nan suka fitoh tare. Ya 'daukar mata sauran kayan da suka suyo yashigar mata dasu

XARAH tana falo tana kallo sai ganinsu tayi da Kaya Tace hmmm Sannunku

YUSUF ya harareta yamaida kallanshi kan LABEEBAH Yace nutsuwata sai munyi waya Tace toh
Yafita XARAH tabishi da dariya tana cewa ajedai mutum saisan luv baxai barmin 'Yar Uwa ta hutaba
Murmushi kawai yayi

LABEEBAH da XARAH ansamu abunda akeso dan haka suka xage suka dinga hira abinsu da yaba kayan da YUSUF yasiya musu

🌵🌵🌹🌹🌵🌵
*MASEEFAR SOO*🌹
🌵🌵🌹🌹🌵🌵

Al'amarin ya farune qarfe taran dare XARAH najikin KAMAL maqale dashi Bayan sungama raya sannu
Tace muje muyi wanka ko ya lakuce mata hanci Yace angaya miki na gama gamsuwa ne
Tashi tayi daga jikinsa tayi toilet tana cewa bara nafarayi kan ka shigo
Murmushi yayi dan ya ganota. Shidai mabuqacine yayinda ita mah takasance gwana wajan yin qoqarin bashi hakkensa da jurewa
Yalura ciki ya kusantota 'dan wata hu'du Amma Sam taqi ganewa dan bata sanibah. Shikuma yaqi gaya mata dan ya lura tsoran cikin take

Toh ganin tashiga toilet yasashi tashi da xuwa jallabiya da niyar xuwa gun LABEEBAH har yakai 'kofah yadawo bakin toilet 'din da XARAH tashiga ya kulleta da key ahankali Sannan ya fitta

LABEEBAH tafito falo kenan dan 'daukar ruwa  taji xuciyarta na bugawa fat fat fat. Aikan tayi wani motsi KAMAL ya 6ullo

_Tace axuciyarta aidama tunda naji xuciyata na bugawa nasan kanne kake tawowa_

Yaxauna ahannun kujera Yana kallanta. Tajuyo ahankali Tace Barka da dare Ya KAMAL
Yace barka da fatan kin ware lafiya
Tayi Murmushi Tace lafiya lau. Sannan tayi Hanyar 'dakin da xata kwanta
Yace jimana 'yan mata
Tsayawa tayi cak
Yatashi yaxo gabanta. tayi saurin sunkuyar  da kanta Yace kalleni
Ahankali takalleshi yayi mata kallan minti 'daya tare da kawar da fuskarshi Yana cije baki dan ya hango MASEEFAR SON shi acikin idannata

yace nine KAMAL 'dinki ko.
Taqara ware idanta akansa cikin tsoro tare da tashin hankali Tace bakai bane Wlhi bakai bane tafa'da daja da baya

Idan kika qara rantsemin akan qarya xan baki mamaki ya fa'di hakan

Ina qaunarki ina qaunarki ina sanki Wlhi baxan barki ba dan ni dake mun dace

Rufe bakinta tayi da hannun damanta tare da sake ruwan data 'dauka aqasa takece da wani gigitaccen kuka
Tana cewa bakai bane naran tse maka ba kai ban.......
Aikan ta qarasa furucinta ya janyota jikinsa ya ha'da bakinsa da nata yahau yimata wani shegen kiss Wanda tunda uwarta ta haifeta bata ta6a sanin lamarin bah
Jikinta ya hau 6ari taxube jikinsa taqara sheqewa da kuka yarabata da jikinsa cikin 'daure fuska Yace nine ko bani bane
Tagirgixa mai kai Tace bakai bane  wlhi narantse
Tauuu..... ya falleta da wani gigitaccen mari Wanda ya gigitatan kuwa Yace nine
Da sauri Tace  Kaine Wlhi kaine

Ya'dago da ha6arta Yace baxan barkiba dan wlhi Aurena dake ba makawa
in kikaga na barki tosai dai im bani ba raina kishirya kar6ar Aurena dan Wlhi baxan barki bah
Yana fa'din hakan ya saketa yayi part 'dinshi

Da gudu LABEEBAH tayi  'daki Tafa'da gado kuka take Wanda kodasu mamah suka rasu batayi kuka irin wannan bah
Ta shiga tashin hankali Wanda batasan ana shigarsa bah
Tayi Allah wadai da xuwanta Abuja

KAMAL ko bu'de XARAH yayi Tace nayi nayi tabu'du taqi kuma nakiraka Naji shuru lafiya Yace bacci nafara yi
Xataqara magana ya rufe mata baki da shigewa toilet 'din

Tana saka kayan bacci tananin lamarin dan taga damuwa afuskar shi meto yafaru daga shigarta wanka
Ta kwanta kenan yafito Tace meya sameka Mijina daga shigata wanka
Ya yarfa mata ruwan hannunshi talumshe ido yace xakimin maganin abunda yake damunane
Cikin sauri Tace eh Yace rantsa kibani kwarin gwiwa Tace narantse.
Yace.......

Washe gari da qarfe 7:00am YUSUF yakira numbar XARAH
Toh dama wayar tana 'dakin da LABEEBAH take batama San da itaba
[7:12PM, 25/09/2016] Rahamat Nalele💋: Kallo 'daya xakama LABEEBAH tabaka tsoro dan ganin yanda fuskarta ta kumbura dan kuka
Wani xaxxa6ine ya rufeta. Wanda tunda take bata ta6a yinsa ba

Tanajin wayan na ringing ta 'dauka dan ganin YUSUF ne Tace hello
Yace haba nutsuwata lefin mena miki kikaqi 'daga wayata jiya
Memakwan tabashi amsa saita fashemai da kuka takashe wayan

XARAH CE tashigo tana kuka wiwi
Tace ban shirya xama da kishiya bah
LABEEBAH

Afurgice ta kalleta
Amma ko kusa XARAH bata kalleta taba
Taci gaba dacewa Ashe haka halin maza yake kiji wai KAMAL Aure xaiji xaiyi min kishiya Auran namu yaushe akayishi

Kuka LABEEBAH taqara fashewa dashi
XARAH nayi itama nayi
Taxauna gefan gado Tace kitemaken LABEEBAH Wlhi ina kishin Mijina ina kishinsa naransa da Allah duk wacce tayi gangancin auranmin miji toko ta kulla qawance da tashin hankali......

Tashi LABEEBAH tayi xatayi magana sai KAMAL yashigo da Murmushi akan fuskar tashi ya kalli XARAH Yace Ni xan tafi. Ko kallansa batayi vah
Ya kalli LABEEBAH gabansa yafa'di Amma ya basar Yace Tafa'da miki yan qara Aure ko
Ta kalleshi
Yaci gaba da cewa Wlhi sainayi auran. Abin takaicin taqi yarda ma taji ko wacece dan nasan xata sota

Amma tunda kun ha'duma shikenan
Bari na fa'da miki ko wacece..........

Ai kamar Aljana LABEEBAH tayi matsugunni a gaban KAMAL dan shi ganinta kawai yayi Tace naroqeka da Allah da manxansa karkace Komai
Kar kama 'Yar uwata kishiya
Karkiyi abinda xaitarwatsa farin cikinta
Karkayi abunda xai dame mu dan Allah.

Ganin irin kikan da LABEEBAH take yasa zuciyar XARAH qara Santa Ashe xata shiga tashin hankali akan damuwarta haka
Sai taji tausayin LABEEBAN ya kamata
Tatashi kawai tafuta
Ganin futarta yasa KAMAL 'dago LABEEBAH Yace idan kinayin irin wannan kukan xaki jamin MASEEFAR dan baxan iya jure hakan bah
Tace kajanye abinda kike sanyi naroqeka
Yace Wlhi baxan janye bah
Hawaye na xubar mata Tace xan kashe Kaina
Yace ba shakka ko xan biki.
Kinga XARAH tarasaki kuma tarasani
Plx ina buqatar farin cikinki kicire damuwa aranki
Yana fa'din haka yafitta saijin tashin motarsa tayi
Aiko taxube agun ta 'dura hannunta aka ta xamba'da ihu
Dai-dai nan YUSUF yashigo gidan da mota Yana fitowa daga motar da niyar shigowa falan
Aiko LABEEBAH ta hangoshi ta windo tafitta da gudu ta rungumeshi tana shash sheqar kuka
Cikin tashin hankali Yace menene meya faru
Fa'di take ya KAMAL ne XARAH CE tana fa'din hakan tana nunamai cikin falan da hanyar da KAMAL yayi

Gaban YUSUF yafa'di hankalinsa ya tashi. Dan ganin kukan da take ba nawasa bane ga fuskarta ta bala'in kumbura duk a furgice take. Tarungume shi tsam

Sai yayi dabarar kama fuskarta ya hau goge mata hawayen. Bala'in tausayinta nacin xuciyarsa
Yace nutsu nutsu nutsuwata plx kwantar da hankalinki ina tare dake
Sannan ya kwantar da kanta agirjinsa tare da maqaleta kamar Yana tsoran kar wani ya kwace mai ita yafara shafah bayanta alamar rarrashi. Xuwa lokacin tadena kukan sai sauke ajiyar xuciya kawai take
Yace Yauwa toh fa'damin meya faru
Cikin wani sanyin murya Tace ya ganoni Ya YUSUF

Ya furta Kalmar SOO agareni

Yana fa'din baxai barni ba

Yana maganar xai aureni

Yana cema XARAH xai qara Aure

Ya wargaxa mata farin cikinta

Tana kuka akan tasan mijinta

Yayinda yanuna halin ku'in kula akan hakan

Ina San XARAH kuma bana fatan tasamu matsala arayuwarta sabodani

Ya xaiyi damu mu biyu Ya YUSUF

Na tsani kaina kuma bana SON shi yanxu.....

Naroqeka da Allah ka kaini gidan mu inga yayana ko gobene
Yayi Murmushi me tattare da tausayi

Yace toh yanxu mubar musu gidansu dan banaso na ha'du da kowa acikin Su.....
Dan xuciyata namin xafi ganina suncutar min da mata daga jiya xuwa yanxu
Tace to bara imma   XARAH sallama da ha'do kayana sai kawai mutafi
Yace mekike nufi
Kina nufin kiqara shiga cikin gidan nan
Saiya girgixa kai alamar inaaaaa
Yace kin barsu kenan har sai igiyar aurena tahau kanki
Taturo baki Tace nabarta fah tana kuka
Yace Allah yasa kukan mutuwa takeyi
Baxakije gareta bah mijinta ya lallasheta

Gya'dakai tayi kawai yajata suka shige motarsa ya ficce daga gidan

Shuru bame magana acikinsu dan dukkansu da abinda suke  kissimawa aranshi. Ita dai LABEEBAH tasaka aranta koxata mutu baxata auri KAMAL ba
Duk da MASEEFAR SOON da take masa

Yayinda xuciyar YUSUF take kukan yanda akayi Yayan nasa ya ankare da lamarin LABEEBAH
Sannan xuciyar tashi tacika da tsoransa  dan yasan yayan nasa sarai kan abinda yakeso
Sam idan Yace yanasan abu tokomiye xaiyi dan yasami wannan abun
Idan kuma yaqi abu tabbas yaqishi har abada
Yanada wasu baiwa Wanda idan ya tunkari abinda yakeso todole wannan abunma yasoshi.

Shiyasa yake katange LABEEBAH dashi
Yasani yayan nashi aikata abu yake abaiyane Sannan baya tsoran takwabe
muddun abin nan bai sa6ama shari'a bah sai yasan yanda yayi yamishi abin

YUSUF ya shafa kansa da sauke ajiyar xuciya yanasan ya ka'daice yayi kuka kuxai samu 'dan nutsuwa a xuciyarsa.
Shidai Yana MASEEFAR SOON LABEEBAH kuma Yana ji aransa idan ya rasata mutuwa kawai xaiyi
Dan tatara duk wani Abu da namiji akeso agun mace LABEEBAH ta ha'du yakar ha'duwa

Direct gidansa na wuse two and utako
Yayi
Gidan me bala'in kyau da tsari kamar na XARAH
Yace nutsuwata ga toilet nan kishiga kiyi wanka bari naje nanemo miki abinda xakici ko
Tace toh idan naci saimu tafiko
Yace baxan maidake gidan Momy yanxu bah sai magrib kannan fuskarki tasauka dan kar Momy taxargi wani kingane ai
Ta'daga mai kai
Yace natuna akwai wasu riguna biyu da muka manta jiya amota bari na'dauko mikisu Tace toh
Tana tsaye anan yakawo mata Sannan ya futa

Wanka tayi tashafah mai da saka turare Sannan tasaka 'daya daga cikin dogayan rigunan daya bata yanxu
Tayane kanta da 'dankwalin rigar
Tayi kyau sosai tafitoh falo tana jiransa

Bata wani da'de da xama bah yashigo. Tsayawa yayi yana kallanta kawai dan inda ace Matarsa CE ba makawa shiyasan irin tarbar da xai mata
Yayi gyaran murya dan ya lura tashiga tunani
Ta kalleshi da sakarmai Murmushi Tace kadawo Yace nadawo nutsuwata kinga yanda kikayi kyau kuwa
Tace kaima kayi kyau sosai
Yace toh gashi saiki gyara nabaki
Tace hmm xanci da Kaina ya kalleta ka'dan Yace baxan iya barinki kici da kanki bah gyara plx nabaki
Tako matsu kusa dashi yadinga bata  tanaci tana xubamai qaramar shagwa6a. Shi kuma yana qara jin tausayinta da santa

Sanda ya tabbatar da taqoshi Sannan yabarta. Tace tokaima tsaya nabaka
Yabi bakinta da kallo abin sha'awa dashi me santsi da laushi ya gya'da mata kai. Tadinga Bashi Suna hirar soyayya lokaci lokaci
Ahaka suka gama
Yace toh xanje Nadawo plx kikula da kanki
Tace. Toh Amma kakiramin XARAH

Ya ta6e baki yaxanyi dake. Ya fa'da yana me danna numbar XARAN
Tace mexance mata
Shuru yamata
Can XARAH ta'dauka
Yace matar yayana Tace na'am katafimin da LABEEBAH ko Yace Ashe kin gammu
Tace eh futanku nagani
Yace gani da nutsuwata ina tattalinta da lallashinta haka kawai kun burkitamin ita dan mugunta.......

Sauke ajiyar xuciya XARAH tayi Tace dan Allah kabani ita inasanjin muryarta ko hankalina xai kwanta Wlhi tashiga tashin hankalin da niban shigaba

Yace naqi bayarwan dama nakira ne dan kisan muna tare kuma xanturo Sagna ta tattara kayanta dana Sumayya gobe tace xata tafi dan baxata iya jure tashin hankalinki bah
Tace dan Allah Yayah YUSUF dan Annabi kabata wayan kaji dan Allah
Yace kinci sa'a gata kuma kikayi wani abunda xaisamin ita kuka Wlhi saidai kijita a Kano dan sallama awaya mah baxaki jita bah

Tace naji bata
Yamiqama LABEEBAH Tace XARAH
Sauke ajiyar xuciya XARAH tayi Tace haqiqa 'Yar uwata ina MASEEFAR SOON Ki
Kishare batun 'daxo dan nayi tunanin kona gaxa tawani gunne yasashi San qara Aure na yima kaina alqawarin xagewa takowane fanni in faranta mishi dan inmantar dashi ita
Inasan Mijina kuma xanso naga wacce yakeso inga abinda yagani agareta Wanda bandashi
Ina SON KAMAL LABEEBAH dan yatara abubuwa daba duk namijiba yayi takota ina inasan shi ina kishinsa plx kitayani da addu'ar Allah ya karkatomin da hankalinsa kaina

Sannan ina rokwanki dakarki tafi gobe
Inaso muqara ha'duwa ko tayayane

Hawaye ya xubuma LABEEBAH YUSUF yamatsa kusa da ita Yana goge mata
Taqer LABEEBAH ta iya CE mata toh jibi ma tafi
XARAH Tace Yauwa ki kwantar da hankalinku fah Tace toh Karki damu......
Sai XARAH takashe wayan

Plx nutsuwata kisoni Ki qaunace danni mesanki
Na miki alqawarin baxaki ta6a Allah wadai dani bah.
Xan baki farin ciki Wanda xai baki mamaki
Kina sona
Takama hannunsa ta sumbata Tace inasan ka kuma kai xan aura
Murmushi yayi Yace toh xumu fitta muxaga gidan ko
Tace toh
Haka yakama hannunta suka fito daga falan

Fasa futar yayi yanemi duk wani abu da  yasan xaiyi dan yaga dariyar LABEEBAH shi yadinga cakalowa
Har ita kanta tagano yanasan tasake tamanta abunda yafaru.
Dan haka sata sake ka'dan

KAMAL ko Yana xuwa office 'dansa ya dasa tunanin LABEEBAH aransa
Duba mutane kawai yakeyi Amma kowa ya duba saiyaga mutanan suna juyemai da kamar LABEEBAH dan haka yace bayajin da'di duk wanda yaxo nemansa yayi hakuri

toh yanxu haka yayi nisa Cikin tunani Auwal yashigo office 'din nashi da sallama Amma ko kusa KAMAL baisan da shigowarsa ba
sanda yata6a shi Sannan ya ankare dashi
Auwal Yace meyake dumunka KAMAL kashiga dogwon tunani haka
Kai tsaye Yace mai MASEEFAR SOO.......

MASEEFAR SOO Auwal
SOO maseefane SOO damuwane SOO ba da'di bane SOO
Tun farkwan ganina da ita xuciyata tacika da bugawa.
dan kowane kallo namata bugawa takeyi har gobe
Natattara duk tunanina nagane yanda nakeji haka takeji itama
Na kamu da MASEEFAR SONTA akwana 'daya
baxan ta6a rabuwa da itabah dan saina Aureta

Tana MASEEFAR SONAH Amma nawa MASEEFAR SOON yafi natah
Wlhi Wlhi Wlhi Auwal idan nabarta ina tabbatar maka ba wata mace da xataji 'da'dina ina tabbatar maka ba wata mace daxanso ina tabbatar maka na ture babun Aure arayuwata dan Itace macen da nake so
itace macan da nake qaunah
Itace idan naji kukanta hankalina yake tashi
itace wacce Komai nata yayimin arayuwa.........

Auwal ya katse shi da cewa wacece wannan yarinyar da burkitaka haka
KAMAL yajah numfashi da tashi ya juyama Auwal baya Yace Aisha-Labibah.....
Aburkice Auwal Yace wacce nasaki 'Yar Uwar XARAH
Ya juyo yace eh ita
itace

Cikin sauri Auwal Yace kuttumar uba

KAMAL ya kallesa Yace kafa'di abinda yafi xagi
Wlhi Auwal bazan ta6a barinta bah

Auwal ya sauke ajiyar xuciya Yace bai dace kaso LABEEBAH bah. Bai kamata bah. Koka manta yanda suke ne in fa'dama........

KAMAL ya katse shi da cewa bam manta ba
Fatima-zarah da Aisha-Labibah yaran da suka tashi da tamkar ciki 'daya suka fitoh dan shakuwa yaran da sukesan junansu
Ko ba haka kake san tunatar dani bah. Ya qarashe da kallansa

Auwal Yace hakane Amma Kasan da hakan kakesan raba soyayyarsu. Kasan kishi kuwa
Yace koma dai miye ba kishiba nifah saina auri LABEEBAH. Dan inasanta ina qaunarta ji nake kamar in kashe kaina akan santa
Jinake kamar na cutar da ita
Meyasa ban gane tana sonah bah
Meyasa da natashi santa nafa'da tarkwan MASEEFAR SOO.
Sam xuciyata taqimin da'di
hankalina yakasa kwanciya
qanqar jinkina yana san ya kasamce da ita

Dama dama dama.
Dama itace XARAH da yanxu take matsayin matata nasan da xan samu nutsuwa
Auwal Yace kadan ne xuciyarka KAMAL karkaxo kayi abunda xai dameku gabaki 'daya
Yace laveeva tarigaka fa'din haka.
Plx kaidai kasani a addu'a dan ina cikin wani hali plx

Tausayinsa Yakama Auwal tabbas ya hango damuwa da tashin hankali agun KAMAL Wanda baita6a ganinsa cikin hakan bah
Yace toh Allah ya fitar dakai
Yace AmEEn nagode
Nan dai suka ta6a hira wacce duk rabinta hankalin KAMAL nagun LABEEBAH
Yace xanje gida kawai Auwal dan samun nutsuwar xuciyata shine ganin LABEEBAH duk da nasan yanxu bata gidana

Auwal Yace toh ba matsala Allah dai ya fiddakai daga MASEEFAR SOO

XARAH na kitchen tana ha'da abincin dare kawai taji dirar motarsa. Gabanta yafa'da
Tanaji yayi 'dakinsa ba kamar yanda yasaba idan ya dawo yabi ta kanta bah

Itama batabi takansa bah.
Taqarashe Komai nata Sannan tajera Komai a dining
Taje tayi wanka tasaka qananun kaya wanda suka amsheta da feshe jikinta da turare Sannan ta nufi 'dakin nasa.
Da sallama tashiga Yana kan gado Yana danna laptop ta xauna gyefansa Tace sannu da

dawowa my luv
Ya 'dauke kansa daga kan laptop 'din yaxuba mata ido
Anan ya 'danga ta'dan xube ka'dan ( *toh kishi wasa ne*)
Saiya ji tausayinta ya kamashi dan koba komai yana santa. Saidai shikansa baisan ya akayi MASEEFAR SON LABEEBAH tamishi illa haka bah daga kwana 'daya duk tabi ta rikitashi ta hargitsa tunaninsa ta jefashi cikin damuwa
Wlhi shi yanxu tausayin kansa yakeji bayajin tausayin kowa sai nasa

Bai ankareba yaga hawaye nabin kuncinta Tace dame narageka my luv
Atunanina duk wani Abu da mace take yima mijinta ina yimaka
Meyasa zaka tarwatsa farin cikina da min kishiya ko shekara bamuyi ba
Bakayi tunanin mutane xasu xargeni bah
Meyasa wannan sauyin yaxomin cikin lokaci qanqani
Saita fashe da kuka ha'de da durqusawa agaban gadan Tace ina rokwanka da Allah kabani wani lokaci xanxage dantse in baka duk wani farin cikin da kake nema.

In yace baiji tausayin XARAH ba yayi qarya
In yace  xuciyarsa batayi rawaba yayi qarya
Amme yafijin tausayin kansa fiye da ita da LABEEBAH

Tashi yayi ya 'dagota tare da xaunar da ita kan jiyarsa Yace banasan in yaudareki XARAH
Ina sanki Sannan xuciyata takamu da Santa
Na miki alqawarin baxaki sami matsala da nibah inhar kika fahimceni
Plx kimin rai ki namince min Auranta dan Allah

Na shiga uku ni XARAH idan ka Aureta baxa kamin adalci bah dan tun yanxu nagano soyayyar da kake mata ta danne tawa. Bansan ya akayi xuciyata tanarke da MASEEFAR SONKA bah
Kayi tako ta ina kowace mace xataso mallakarka amatsayin mijinta
Katemaken xuciyata dan tanamin xafi hankalina na tashi da xaran na hangoka da wata mace.
Plx katemaken kabani lokaci Wlhi Xanyi duk wani qoqari dan mantar da kai wata *'YA MACE*
Taqarashe da rushewa da kuka
Rungumarta yayi shima hawayan yaxubu mishi Yace am sorry najiki xanyi qoqari inga koxan iya barinta Amma gaskiya TEEMAH da kamar wiya............

YUSUF da LABEEBAH ko sai kusan biyar suka yi gidan Momy
Zuwa lokacin LABEEBAH tasake dan kam YUSUF yayi qoqari wajan sata farin ciki
Anan taga kayanta dana Sumayya da sagna ta 'dauko a gidan XARAH

Can wajan qarfe 8:00pm na dare KAMAL ya shigo gidan direct 'dakin Momy yayi

Nan yaganta da Safna Suna linke wasu sababbin Kaya Momy nace mata maxa jeki kiramin LABEEBAH Tace toh xata fita
tagai sheshi ya amsa cikin kulawa Sannan ya gaida Momy
Taxumai ido dan ganin yanda yaxama wani iri bayi da maraba da mara lafiya
Cikin tashin hankali Tace mexan gani haka KAMAL meya sameka meyake damunka kaga inda kaxube kuwa........
LABEEBAH CE ta shigo da sallama idanta ya sauka akan KAMAL gabanta yafa'di.
Momy ta'amsa sallamarta KAMAL ko Sam baiyi gigin kallanta bah
Tace banasan rabuwa da XARAH ne
Kuma nasan Ya YUSUF xai iya riqemu amana
Momy tayi dariya da girgixa kai dan tagano quruciya na damun LABEEBAH
Dan haka cikin siyar siyasa Tace niko da kinbar XARAH ta auri wani dan xaman Aure xa kuyi ba wasa bah
Ina ganin baxaku sami xaman lafiya yanda ke kikeji aranki bah
Xuciya bata da qashi LABEEBAH kuma yau da gobe tafi qarfin wasa.
LABEEBAH tayi shuru
Can Tace Wlhi momy xamu xauna lafiya tana sona ina Santa fah
Momy ta girgixa kai Tace shi YUSUF Yace miki Yana Santa ne
LABEEBAH ta girgixa kai hawaye nasan xubu mata
Momy tajah numfashi da danna number YUSUF a wayanta dan kira. Aiko nan take ya shiga
Ya 'dauka Yana fa'din my mom
Kaxo falo kasaman yanxu.
Toh Yace da kashe wayan
Ko cikakken motsi basuyi ba yashigo falan da xama kusa LABEEBAH Yace gani mom
Tace LABEEBAH taxomin da xancan tana SO ka Aureta da XARAH shin ya kagani

Ya waro ido😳 Yace Wlhi bala'i nagani mom
Plx Karki biye wawiyar yarinyarnar
Ban ta6a jin XARAH araina ba
Akanme xan Aureta......

Aiko saijin kukan LABEEBAH sukayi takama hannun YUSUF Tace dan Allah dan Annabi
Yayana ka Auremu mu biyu naroqe da Allah
Yace Waike me yake damunki ne kishiya xan miki fah 😳
Tace toh ai 'Yar uwatace kuma ba xamuyi xaman kishi ba... Takai kallanta ga mom da tasake baki tana kallan ikwan Allah
Tace dan Allah Momyna kisashi ya Auremu mu biyu plx

Taqara Jan numfashi Momy tayi Tace toh naji 'Yata yaushe kikesan ayi bikin
Cikin murna Tace idan XARAH ta yaye SAUBAN. Ko Momy

Momy tayi Murmushi da gya'da kai  Tace toh yanxu sai ada'da 'daga bikin. YUSUF ka shirya
Auransu Su biyu ankashe wannan xancan kikwatan da hankalinki kinji 'Yata
LABEEBAH tayi Murmushin jin da'di Tace toh Momy xamu tafi Tace tun yanxu

Labeebah tace Aunty Rukayya batajin da'dine banaso nayi nesa da ita
Momy Tace Yana kyau hakan. Ta kwallama Safna kira
Sai gasu dukkansu da Sumayya.

YUSUF ko kukane kawai bai sake bah. ranshi ya bala'in 6aci Amma yacije ya tashi Yace ina jiranku amota da sauri LABEEBAH Tace toh

Sukaje sukama Kakah sallama
Momy tabi LABEEBAH da kallan tausayi dan taso ta mallaki YUSUF ita 'daya dan tasan xai gina musu rayuwar da xusuji da'di kuma ya hucce mata takaicin wasu al'amuran

A motar ko bame magana
Candai Sumayya tagaji da shurun Tace Aunty LABEEBAH wai yau yana jiku shurune bamai magana acikin ku
Shuru LABEEBAH tayi mata
YUSUF yayi murmushin yaqe Yace kekuma gwulma ko
Tayi dariya Tace Wlhi ba gwulma bane Ya YUSUF kawai naga ba haka kuka Saba bah

Yace Auntyn naki ta6amin raine
Tace ayya kayi hakuri dan Allah ka yafe mata tayine bada saninta bah
Murmushi yayi Yace Karki damu Sumayya xanbi hanyar daxan hukuntata dan baxan barta haka bah
LABEEBAH ta kalleshi aiko suka ha'da ido ya sakar mata murmushin mugunta

Sumayya Tace kai ya YUSUF baxa dai ka hakura bah
Yace Wlhi kuwa Sumayya
Dai-dai nan yayi faking kofar gidan nasu Sumayya tafita tana yimai mungode ya 'daga mata hannu alamar Bakomai
Sainnan ya juyo da kallansa ga LABEEBAH Yace toh Uwar gida ya akayi ne
Tace plx MeeNi karka cutar dani akan abinda tausayine yasani aikata Komai
Yace kinga Uwar gidana kwantar da hankalinki ba wani abunda xan miki. Kawai inasone Ki gayamin kalmomin da xanji cikin raina susani nisha'di ako yaushe idan na tunasu
Tayi shuru .
Yace no fah inkin shiga wani hali karkice Komai. Bani numvar XARAH kinga inna nema agunta nasan baxata jamin ajiba
Gaban LABEEBAH yabada dam takalleshi ya kashe mata ido
Cikin sanyi Tace I luv u
Yace shikenan
Tace toh Xanyi missing 'dinka MeeNi
Tana fa'din haka tafitta daga motar tashige gida. Ya bita da harara xuciyarshi na mishi xafi akan yanda ta qaqaba mishi XARAH gashi ya shirya musu rayuwar da yakesan suyi yanxu ta6ata mishi shiri

Koda yaxo Washe gari jona mata hauka yayi yabarta

Abin da ya faruko shine bayan sungama gaisawa
Yafara maida hankalinsa ga 'kofar gidansu XARAH
Tace me kake kallo ne Yace Wlhi XARAH ce nakesan tafitoh in ganta ko nasamu Sauqin xuciyata
Tace what 😳
Har kafara santa ne
Yace eh sosaima ayanxu ke da ita bansan wacce nafi sobah
Tun jiya dana koma gida hotanki da XARAH na 'dauko ina gwada acikin ke da ita wacece tafi kyau
Ashe tafiki kyau ke'din axuciyata kawai kike
Gaskiya XARAH ta ha'du inasan tah sosai
Kuka LABEEBAH ta fashemai dashi dan Wlhi wani irin 6acin raine ya kamata Wanda inxa'a kasheta baxatace ga abinda yasa bah
Cikin nuna tashin hankali YUSUF ya janyota jikinsa yana cewa me ya faru
Tace nidai kadena min xancan XARAH
Yace oho XARAN taki kuma yau itace bakya san amiki xancanta
Ta 'dagamai kai
Yayi Murmushi yace toh baxan qaraba.
Haka yata lallashinta daya tashi tafiya harsunyi sallama takai 'kofar gidansu ya biyota Yace tabashi number XARAH
Miqa mishi wayanta tayi kawai
Tana takallo yaciri numbar haryana matsowa kusa da ita wajan rubuta suna
Itako har tana leqawa taga sunan daxai sah
Nan taga yasa *farin ciki na*
Sai yanuna mata numbarta Yace kinga ke *nutsuwata* ita kuma farin cikina. Yayi dai-dai ko nacanjah
Cikin Takaici ta kar6i wayan nata tayi cikin gida da gudu
Shiko cikin 'daga murya Yace nutsuwata banji an kiraki bafah.......

Ko kulashi ba tayi bah
YUSUF yayi murmushin mugunta ya shige motarsa ya tafi

Tuqi yake Amma fa"di yake aransa ina sanki LABEEBAH ina qaunarki
Amma Baxan ta6a yafe miki akan yanda kikesan ha"dani da XARAH bah. Xan hukuntaki dan in

gyara miki tunaninki

Tun daga ranar YUSUF yasaka LABEEBAH agaba
Duk abinda yasan idan yayi xai cakalo kishinta shi yakeyi. Haka xai saita kuka kuma ya lallasheta Amma bashi xaisa anjima ya kuma sata ba
Ga shi yaqi yarda Sam ya ha"du da XARAH dan baya buqatar hakan
Amma sai ya dinga nunama LABEEBAH kullun suna tare da XARAH a waya Suna hira

Gaskiyane  LABEEBAH na ganin ayah arayuwarta
Yanxu ciwan kishin YUSUF ne yasata agaba
Haushin XARAH takeji kamar ta shaqeta Amma saboda iya xama da Mutane ko afuska bata ta6a nunama XARAN ba

Abinne ya ha"du mata biyu

Na farko takasa mantawa da KAMAL dan kullun saitayi kukan rashinsa cikin dare
Batayi wasa da wata sarqa me zobe da abin hannu dashi KAMAL 'din ya ta6a siya musu ita da XARAH ba.
Kullun kallan zoben takeyi tamkar shi KAMAL 'dinne ya saka mata ahannunta
Takan 6ata lokaci wajan Ganin hotansa
Takanyi kuma dariya idan ta kalli SAUBAN

XARAH tagama shaqer LABEEBAH aranta dan ba wacce ta tsana aduniya kamar LABEEBAH

Tsanarko taqarune saka makwan 'dauke qafar da YUSUF yayima gidansu
Dama tahakanne take samun Sauqi axuciyarta
Dan Ganin shine samun nutsuwata
Amma ya 'dauke qafah
Ko zuwa yayi saidai yasaka Sumayya ta kar6o mishi SAUBAN in lokacin baya gun LABEEBAH

LABEEBAH ko saidai tata6e baki Tace kana wani alaye kashiga gidan da kanka mana ko bakwan kane yanxu gidan
Yakanyi Murmushi Yace hmmm MASIFAR SON da nakema XARAH bata kai nan ba nutsuwata.

kema kyayimin fa'da haka kawai nashiga ga sirikata
Ko kin manta yanxu innah suruka tace

LABEEBAH takanyi shuru dan yanxu YUSUF ya canja mata gani takeyi ya dena Santa XARAH ya keso. Hakanko yana sawa taqara jin haushin ~*XARAH*~

*Bayan shekara biyu da watanni*

Haka rayuwar tasu taketa tafiya yau taxo ma LABEEBAH da da'di gobe kuma 6anin haka. ga kowa mah aduniya rayuwar da yakeyi kenan .

XARAH ko sai abinda yaci gabah ita da Hajjiya Turai.

Inda ita Turai 'din tafara nunama XARAH toh fah lokaci yayi daxaki fara aiki da maka manki XARAH

XARAH ta girgixa qafah Tace tunda na yayaye SAUBAN bah

Turai Tace madallah kinga yanda kike kuwa. Wlhi kamar bakiyi Aure kin haife SAUBAN bah

Kinga kayan nan maganin matane na haqiqa na mallaka awajan wani hamshaqin malami na kar6o dan kaf magungunansa bana banxa duk tsiyar namiji ya kusan ceki ya rufe shafin wata mace kenan.
Wlhi ina tabbatar miki idan kikayi amfani da wa'yan nan narantse miki YUSUF baxai kalli LABEEBAH ba
Dan kin tarwatsa soyayyarta axuciyarsa har abada
Musumman inya kusanceta kin san Allah yabar kusantar kowace 'ya mace aduniya in ba kebah
Ace shi mebin matane to daga ranar ya barsu har abada
Dan kallansu xaiyi tamkar maxa 'yan uwansa

*XARAH tasheqe da wata shegiyar dariya suka tafah*
*Tace an gaya miki ni wawiya ce da xan bari YUSUF yasan LABEEBAH.*
*inaaaaaaa.*
*ta girgixa kai*
*Taqarashe da cewa Wlhi Matarsa mah* *Allah ya 'dauketa ne dan in mallakeshi Ni 'daya*

*Kawai xan so ya Aureta ne saboda surutun Mutane karsuga abayi mata adalci bah*

*Idan muka kasance matansa ko tayayane saina rabata dashi ita dashi saidai ido👀*

Kinga idan na 'dan 'dana mata axabar sanshi datayi saina San yanda Xanyi insashi ya rabu da ita Jameel ya Aureta Kinsan wannan yana cikin game 'dinmu nida shi.
Turai ta waro 😳 Tace kin Allah na manta dashi
XARAH Tace niko ina xan manta dashi
Turai tajah numfashi Tace danayi wani tunani mexai hana kibarta da Jameel sai musan yanda xamuyi kisami YUSUF ke 'daya
XARAH ta gyara xama Tace har yanxu kin kasa fahimta
Auran LABEEBAH da YUSUF tamkar ba Aure bane
Dan xan bari ta Aure shine saboda mutane
Kuma ba abinda Auranta dashi xai taremin.
Saimani daxan tare mata shi

Ina tabbatar miki kan aje ko ina xata nemi ya saketa
Ni kuma Xanyi ammafani da wannan damar in ingixa xuciyarshi ya rabu da ita Jameel ya samu

Turai ta 'daka mata duka Tace gaskiya  XARAH baki da alqawari. Xuciyarki abushe take. Dan imanin naki ya tafi. Ixuwa yanxu har nafara tausayin LABEEBAH Wlhi

Bakiyi halin *Nana Fatima* bah
Macan da babu kamarta aduk duniya
Macen da bata da mugunta macen da.........

XARAH tayi saurin katseta da cewa Allah ya bamu albarkacinta

Eh inada nawa halin Amma kome nayi ke kika 'dorani akan hanya
Amma kinnasan cewa wani......

Turai itama ta katseta da cewa naji abin baikai nan bah koma me kikayi MASEEFAR SONE yaja miki haka

Yanxu saura wata 'daya bikin naku baki ban labarin yanda aka karke da Innah bah
[12:41PM, 06/10/2016] Rahamat Nalele💋: XARAH Tace hmm Wlhi da har nayi tunanin ko Innah ba sona takeba

Turai Tace meyasa
Tace yanda tanuna Allah ya karta ya binne baxan auri YUSUF ba dan na LABEEBAH ne
Baban mu ya biye mata ko
Ita kuma shegiyar taxo tasaka Su agaba da kuka da magiya akan ita taji tagani ya Auremu mu biyu batasan rabuwa da nine

Bu'dar bakin innah Kinsan me tace mata
Turai ta girgixa kai
XARAH taciga da cewa
Cewa tayi wai tarufe mata baki ita bata da hankali
Akanme xata CE YUSUF ya Aure Ni
LABEEBAH tagyara xama tadinga jero mata misalai akan batasan ta rasani kusa da ita muna san junanmu dan Allah tah bari ayi auran

Momyn YUSUF nagun akayi Komai daqer da si'din gashi Innah tayarda

Kinsan Allah agun sanda soyayyar LABEEBAH ta motsamin  Santa ya manayemin xuciyata
Amma da YUSUF yakira awaje dan suta6a ta'di nan take tsanarta ta dawomin

Turai tayi dariya da cewa yanxu innah ta yarda kenan
XARAH Tace eh kai ba dole bah
Dan LABEEBAN da Momyn YUSUF ne suka sukata a gabah da magiyar har tayarda
Washe garin ranar iyayan YUSUF suka kawo sadakina.
Toh kinji Komai

Turai Tace toh madallah
Yanxu dai yau xaki fara amfani da magungunan nan
Dama na wata 'daya kinga duk ranar da YUSUF yayi gangancin ta6aki ko uwarsa qarya take ta rabaki da shi

Al'amarin auran nasu yaxo da salo
Yau saura sati 'daya.....☝🏻jal

Amma XARAH ta nunama LABEEBAH karsuyi Komai
Yayinda LABEEBAH Tace ko walima baxa muyi ba
XARAH Tace toh duk yanda kikace haka xa'ayi
LABEEBAH ta girgirxa kai Tace aa karmiyi Komai 'din

Sumayya najinsu
Itadai tarasa dalilin  da yasa. Talejin haushin 'Yar Uwar tata XARAH
Gani takeyi ta cutar da LABEEBAH
Akanme xata yarda da ha'din da LABEEBAN tayi bata tirjeba
Sai kawai ta tsinci kanta da jan tsaki
Rukayya tata6e baki

XARAH da LABEEBAH suka bisu da kallo
XARAH takasa hakuri Tace wai meyake damunki ne Sumayya kwana kinnan kin canja daga kijah tsaki saiki dinga hararata
Rukayya Tace qila kinyi abinda bai dace bane
Tace menayi Aunty Rukayya fa'damin
Tashi tayi tana shanya Tace inaxan sani XARAH gaki ga Sumayyan ita xaki tambaya ai Saitajah tsaki Tace banyi Komai ba. Inadai ganin iskancine kawai yake sata haka
Rukayya tace hmmm ba mamaki

Da yammar ranar ne
Rukayya tayi qoqari wajan tursasa LABEEBAH shan tsumi na mata da abinda baxa'a rasabah
Fa'di take Kinga XARAH tayi Aure tasan me yafi da'di a Aure da abinda yake kawo matsala
Ba xama xatayi YUSUF yajita salam bah
Dan haka kema kidage da shan kayan marmari da wannan tsumin
Toh LABEEBAH Tace mata dan tun safe barartace take mata ciwo ka'dan ka'dan

Abin bai caf keta da kyau bah sai gab magriba
Nan ta nemi  sumewa Usman ya furgita dan yasan yanda ciwan nata take
Ya shiga 'dakinsa dan tuna wani magani da wani me magani yabashi Yace insha Allah inya tashi mata tajiqa tasha xata samu lafiya
Cikin sauri Rukayya ta ji'ka maganin suka bata tasha. Nan bacci yayi awan gaba da ita
Bata farkaba sai kusan asubah takoga al'adar

Sumayya tayi mata sannu Tace kina buqatar wani abune
Tace aa
Nan tatashi sai tajita garau sumul
Saidai tana 'danjin ciwan ka'dan
Da tayi karin safe Usman ya qara bata tasha.
Rukayya Sumayya Innah XARAH duk sata sukayi agaba Suna yimata kallan tausani

SAUBAN na maqale da ita fa'di yake cikin gwarancinsa yana cewa me yasameki momyna
Ta shafah kansa Tace bani da lafiya SAUBAN Amma na samu Sauqi
Saiya kwanatar da kansa a qirjinta yayi lamo

Innah taja numfashi da kallan Usman Tace aiko tunda yayi mata magani ka qara kar6o mata ta ajiye saboda wata ranah
Yace akwai da yawa nama bata. dan me maganin baya xama yau yana wannan gari gobe yana wannacan
Innah Tace Allah mah ya rabata dashi gabaki 'daya
AmEEn duk sukace

Da yamma Momy ta aiko wasu attajirai mata da kayan Auran LABEEBAH dana XARAH Komai iri 'daya Kaya masu kyau da inganci da sha'awa

🌵🌵🌹🌹🌵🌵
~*MASEEFAR SOO*~🌹
🌵🌵🌹🌹🌵🌵

Toh yau dai alqawarin ya cika
*An 'daura Auran YUSUF da LABEEBAH & XARAH*

Me xai faru 😳
Bayan Amare sunsha nasiya sunsha kuka

'yan kaisu sun luluqa dasu Abuja inda suka diresu a gidan Momy suka Sha nasiyarta sai suka kwashesu suka kaisu tangamemen gidan inda yaba mutane sha'awa
Dan part 'din XARAH daban na LABEEBAH daban saidai akwai wani falo atsakaninsu Wanda xai sadasu da juna in sunso

Wannan aikin Dadyn YUSUF ne dan shi yasa aka Komai tunda yaji maganar 'dan nasa Su biyu xai aura yasa aka hau gini ahankali har aka gama Komai

Haka Mutane suka musu addu'ar xaman lafiya sukayi gidan Momy acan xasu kwana
[1:28PM, 06/10/2016] Rahamat Nalele💋: YUSUF ko yana tsakiyar abo kana yansa. yayi musu shuru yanajin tsiyar da suke masa yau xai qara angwancewa
Salim 'dan uwansa Yace toh 'dakin waxai fara shiga oho
Yace LABEEBAH bah
'Daya daga cikinsu Yace habah dai kasani tunda akayi maganarka da XARAH batakayi gigin da kasake ha'duwa da itaba ko ka ganta kanta ankare da kai kakeyin fuska
Yace hmm kunga xaku rakani ne ko in tafi da Kaina

Sukace wane mu sai munje munga kwul Uwar dakah

XARAH safa da marwa daketayi cikin bet room 'dinta jiki ya jiqa da magani yana buqatar maxa Fa'di take aranta Allah yasa yafara shiga gun LABEEBAH yana xuwa gunta ta rufe kofah shikenan baxai koma gun LABEEBAH bah. A sannan in Komai ya wakana ta tarwatsa tsakanishi da LABEEBAH

LABEEBAH ko tsoro ne ya shigeta hankalinta yatashi tasani ba makawa YUSUF agunta xai kwana tana tsoran mexai biyo baya itadai batasan ya abin yake bah Amma acan baya XARAH ta ta6a gaya mata ba da'di har sumewa mutum yake

Dariyace ta kamata data tuna tanamah period me xai mata mah tana cikin jini
Wata xuciyar tace mata ba gobe xaki gama bah
Abayyane Tace ba gama XARAH bah.......

Shugowar YUSUF ne ya katseta da xama kusa da ita Yace iye kaga Uwar gidana
Ta harareshi
Yajawo ta jikinsa Yace yau kin xama tawa nutsuwata. yau xan bu'de miki wata rayuwa. Baxaki qara ciwan marar da kikeyi bah
Shuru tayi mishi
Shima shurun yayi can Yace nabar mutane a Babban falo tashi muje Su muku Nasiha
Ta'dan bugi qirjinsa takai harda kai
'Dago fuskarta yayi yakai bakinsa cikin nata ya hau yimata  kiss baji ba gani.....
Can wayarsa tayi qara. Hakan yasashi barinta
 tako langwa6emai ajiki
Ya 'dauki wayan idanshi alumshe
Salim Yace xamu tafi kasa in kira XARAH ka kuma shanyamu kamar kayan wanki

Xare LABEEBAH yayi daga jikinsa ya miqe da riqo hannunta Yace muje
Ahaka sukaje har falan hannunshi Cikin nata taxauna kusa da XARAH
Nan abokanaye suka hau addu'o'e dayi musu fatan alkairi dasu xauna lafiya
Sannan suka ajiye musu kaji da madara suka tafi
YUSUF yadawo da kulle falan bayan ya rakasu

XARAH Tatashi tana cema LABEEBAH saida safe
Bata jira cewar LABEEBAN bah tayi part 'dinta YUSUF ya bita da kallo
LABEEBAH ta kalleshi ka'dan ya kashe mata ido 'daya Yace bara inje imma XARAH saida safe sai inxo ko
'daga mai kai tayi
Ya qaraso da saka hannunsa ya shafi fuskarta ka'dan Sannan yayi part 'din XARAH
Ita kuma tayi part 'dinta

.
[2:55PM, 06/10/2016] Rahamat Nalele💋: Abune wannan bai saba dashi bah
Abune Wanda yake tunanin ta ina xai fara yinshi
Shiyasa da ya shiga bet room 'din XARAH ya xauna gyefan gadanta yayi shuru
Itama da take kan gadan shuru tayi xuciyarta nayi mata xafi yanda 'daxo yaje ya da'de a 'dakin LABEEBAH Uwar me ya tsayayi

Can dataga  shurun yayi yawa saita fashe mai da kuka wiwi
Hankalin YUSUF yatashi sai yarasa yama xaiyi da ita
Yasani in LABEEBAH namai kuka saurin ha'data yakeyi da jikinsa nan xata mishi shuru
Amma XARAH dako hannunta bai ta6a riqewa ba ya xai mata
Tashi yayi yadafe kansa Yace kiyi shuru dan Allah
Aiko taqara rushewa da kuka.......

Shikansa tsintar kansa yayi agabanta ya rungumeta still bata dena kukan bah
Ciro hankicif 'dinsa yayi yana gige mata hawayan
Yace plx XARAH kiyi shuru meya faru Tace meyasa baka sonah
Jin Kalmar yayi tamkar saukar aradu da kah
Yace ina sanki mana Tace ban yarda bah dan kafisan LABEEBAH dani
Shuru YUSUF yayi yarasa me xaice mata
Itako taxare jikinta daga nasa taci gaba da kukanta
Yaqara dafe kansa yana kiran sunan Allah Yace yanxu me kikeso na miki na nuna miki ina sanki
Tace sonake ka kwana anan dan ina bala'in furgita inna kwana ni 'daya ni bakamar LABEEBAH bace da bani tsoro
Da sauri ya kalleta kana yajah numfashi yayi shuru kawai yana kallan qasa
Can Yace toh bari nafa'dama LABEEBAN saina dawo
Matsowa jikinsa tayi tashige mishi ta fara kuka tana cewa Wlhi LABEEBAH ba Komai xatace bah tasan halin tsorona plx karka futa in ka fita sumewa xanyi dan hakama 'daxo naga kamar mciji ya wucce
Shuru YUSUF yayi danjin wani furgitatcan qamshi dayake shaqa daga gareta wanda yasa yafarajin kanka na juyewa wani maseefaffan filing na na sha'awa na kusantoshi.
Sai tsintar kanshi yayi da rungumarta yafara kissing 'dinta tako ta ina
Sanda ya samu nutsuwa na kiss 'din Sannan ya rabata da jikinsa yayi toilet dayin wanka da alwala
Bayan yafitoh Yace itama taje tayi
Kafin ta fito ya canja Kaya
Dake tunkan suxo tayi wanka sai kawai ta'dauro alqala suka hau lafula raka'a biyu dayin
Addu'a Sannan ya 'dauko mata kaxarta da madara yasa a gaba sukaci ka'dan yanata mamakin kansa da ita.
Bayan sun gama XARAH tayi gado
Ba wani nuqu nuqu YUSUF yabita

Ya rabata da Komai nata ya hau sarrafata kamar injin
YUSUF yaga bala'i da MASEEFA ganin idansa ya kasa gajiya da XARAH Sam
Yi yake Amma yaqi barinta

Itako sumewa tayi dan batayi tunanin aika aikan da tayi xaikaita hakaba
Can YUSUF ya fashe da kuka danjin wani MASEEFAR SON XARAH daya cafki xuciyarsa
Badan yaso ba ya barta dan karya illata kansa
Xuba mata ido yayi kawai yana kallanta SOONTA na shigarsa

LABEEBAH fah😳
Gani tayi shuru YUSUF bai dawo bah taje tayi wanka tasaka kayan bacci tayi addu'a da kwantawa abinta sai bacci yayi awan gabah da ita
Ta cikin baccin natane tayi mafarkin KAMAL

_cikin wani ni'iman taccan gida me kyau_
_Yana wajan furanni Sai qamshin furannin ne me tashi agun_
_KAMAL yana xaune kan sallaya yana addu'a Amma batasan me yake cewa bah_
_Ya juyo ahankali suka ha'da ido_
_Wannan abun dayake fitowa a idansa ya shiga nata idan shi yafitoh daga idan nasa ya shiga natan_
_Ta lumshe ido Tace Ya KAMAL wata duniyace wannan._
_Yayi Murmushi ya nuna mata wani gu da hannunshi. Tabi gun da kallo_
_XARAH tagani da YUSUF maqale da juna. Amma hankalin YUSUF nakanta dan sai miqo mata hannu yake alamar daje gare shi yana hawaye still yana rungume da XARAH_

_Saiko ta maqale kafa'da cikin tsoro Tace baxan xo bah_

_KAMAL yayi Murmushi da girgixa kai Yace plx Babyna kibarsu ahaka Karki shiga rayuwarsu_
_kijirani kiriqemin alkawarin kanki_

_Nufu shi tafayi. Saidai wani xare me qarfi yayi mata katanga da_ _KAMAL Tace dan Allah Ya KAMAL kaxo kayanke igiyarnan kar Ya YUSUF ya kamani_
_Yace bani da damar yanke igiyar_....

Furgigit LABEEBAH tafarka lokacin yayi dai-dai da qala kiran sallar asubah.

🤔 Amma fah kumin afuwa masu xagina Nagode
Sai dai inasan kusani baxan canja tsarin littafina bah

Fa'di take aranta  nariqe maka alqawari Ya KAMAL
Sannan kuma kar in shiga rayuwar XARAH YUSUF
In jiraka
Me hakan yake nufi
Shuru tayi xuwacan xuciyarta tacemata kishare kawai karki sakama kanki damuwa ai mafarki ba gaskiya bane

Aiko tatashi tayi toilet ta gyara jikinta dayin wanka kana ta share falan nata duk da bawani datti bane dashi
Ta fesa turara. Sannan. Ta koma ta kwanta tana tuna YUSUF daga cewa bari yayima XARAH saida safe Amma shuru

Bayan YUSUF ya tsaftace kansa yafitoh ya'dan yarfama XARAH ruwa
Aiko nan ta farfa'do da jan numfashi
Ya xauna gyefan gadan yana kallanta Yace in 'daukeki in miki wankan ne ko Yah

Ta harareshi tare da tashi tayi toilet ahankali dan ta 'dan 'dana ko'darta

YUSUF yayi Murmushi Yace yanxu aka fara

Koda tagama tsaftace nata jikin  xama tayi a toilet 'din tana rayawa aranta eh Lalle YUSUF bashi da imani
    Tun take da KAMAL bai ta6a bata wahala irin yanda YUSUF ya bata yau bah

Shurun yayi yawa inji xuciyar YUSUF
Dan haka sai kawai yafa'da toilet 'din
Aiko ganinta yayi cikin tunanin
Yace Kinga malama ke nake jira
Tace Menene
Dariya yayi dan Ganin yanda ta tsorata
Ya qarasa shiga toilet da kamota suka fitoh da kwantawa
Nan ya rungume abinsa
XARAH dai Tace tayi kwanan farin ciki
Yayinda YUSUF yayi na Mamakin kansa da ita
Farkawar YUSUF yayi dai-dai da farkawar LABEEBAH da Asuba haka yatashi XARAH sukayi Sallah

Washe gari kusan qarfe takwai Momy ta tauro musu su Sagna da Safna da breakfast

Shashin LABEEBAH suka farayi. Dake kofar abu'de take sai suka shiga kawai
Nan suka ganta kwance tana bacci hankali kwançe
SAUBAN ya saki hannun Safna yayi kan gadan da gudu ya 'dane da hawa kanta yana dariya
Ai nan LABEEBAH Tatashi da sakar musu Murmushi
Tace yaushe kukaxo
Suka gaisheta Sagna Tace yanxu mukaxo
Safna Tace kinsan kukan da yarannan yamana agida kowa
Sagna Tace Wlhi hanamu bacci yayi
Wai shidai mamansa akaisa gun mamansa
Aiko Momy Tace mutawo dashi ya xauna gun wacce batada da Ya YUSUF
LABEEBAH taqara rungumarsa Tace ai kun kyautamin da kuka kawoshi ina kayansa Sagna Tace yana falo
Tace Yauwa da kama fuskarshi Suna wasa

Safna Tace breakfast muka kawo
LABEEBAH Tace toh Sannunku.

Nan suka ta6a hira kana sukayi part 'din XARAH dan gaisar da ita
Da sallama suka shiga falan shukaji shuru
Sagna Tace mushiga bet room ko itama baccin take
Safna Tace baki dakai bakiga bamuga ya YUSUF a 'dakin Aunty LABEEBAH qila anan ya kwana
Sagna Tace anya mudai shiga. Safna tayi waje tana cewa Wlhi baxan shigaba
Aiko Sagna ta leqa ta windan Bet room 'din
Nan taga XARAH maqale ajikin YUSUF Suna bacci hankali kwance
Futuwa tayi itama Tace mah Safna dagaske Suna tare Wlhi xoki gansu  Safna tace bacci suke Tace eh
Nan itama Safna taje taleqasu
Suka fito Suna dariya dayin gun LABEEBAH sukace Ashe basu tashiba
LABEEBAH Tace suwa Sagna Tace Ya YUSUF da Aunty XARAH man mun leqasu sai bacci sukeyi hankali kwance
Gaban LABEEBAH ya tsinke ya fa'di dammm
Tayi saurin qaqalo Murmushi da kallan agogo ganin takwas da rabi Tace  yanxu xasu tashi
Safna tace mu xamu tafi Aunty tace mungode kugaida momy suka toh xataji dayi mata sai anjima suka tafi

Akan hanyarsu ne Safna Tace Wlhi naxaci ya YUSUF agun Aunty LABEEBAH xai kwana
Sagna Tace nima nayi tunanin haka Amma kamar baidace abinda yayibah
Safna Tace ina ruwanki kika sani ko ita Aunty LABEEBAN CE Tace yaje guntan kin santa da gwaninta
Sagna Tace aikowa akwaita da gwanintar Allah yasa karya xame mata matsala dan Wlhi Aunty XARAH tafita wayo kuma Kinga shi namiji kamar kwallo yake duk wacce ta iya cillashi itace dashi
Safna Tace toh malamar soyayya kice Aminu har yanda xaki mallakeshi ya koyar dake
Sagna Tace eh aimu xaman Auran mu da kallo
Safna Tace xa'asha kalle kalle ba kallo bah
Sagna tajah tsaki

LABEEBAH tashiryama SAUBAN kayansa tsaf a durowa
Sannan. Suka baje sulayi breakfast 'dinsu kana taje Babban falo tajera sauran a dining Sannan suka dawo suka da'da bajewa itada SAUBAN 'dinta tadinga biyema shirmansa.
Amma hankalinta yana kan XARAH da YUSUF abin ya bata mamaki yanda taji Su Sagna sunce wai har yanxu bacci suke basu tashi bah.
Me hakan yake nufi
Yana nufin anan ya kwana abinsa. Xuciyata tabata amsa

YUSUF da XARAH sai xuwa goma suka tashi
Sukayi wanka
YUSUF yafitoh falo yanata mamakin Kasan cewarsa da XARAH

Can tabiyoshi falan tagaidashi idanta a qasa
Ya amsa da kulawa sai kuma sukayi shuru
Dake YUSUF yasan kan tamace tashi yayi yaxo gabanta ya durkusa Yace farin cikina kisoni plx kamar yanda nasoki na qaunaceki adaran jiya
Fashewa da kuka tayi Tace inasanka YUSUF son da wata mace bata ta6ayi maka shiba
Nafa'da ~*MASEEFAR SONKA*~ saidai xan kasance cikin damuwa da tashin hankali ha'de da baqin ciki
Ya share mata hawayanta Yace fa'damin me xai yawo miki haka
Tace kishinka ne xai jawomin haka
Inasan 'Yar uwata LABEEBAH Amma akan kishinka xamu samu babbar matsala da ita dan baxan iya jure kaje gareta Sannan kaxo gareni ba
Xuciyata xata iya bugawa
Taqarashe da rushemai da kuka
[8:19PM, 08/10/2016] Rahamat Nalele💋: --------------
Ba qaramin bugawa xuciyar YUSUF tayiba. atake hankalinshi yatashi. Sam ya manta da LABEEBAH tunda ya shiga 'dinkin XARAH jiya
Tashi yayi ya dafe kai Yace innalillahi.......
XARAH Tace wani abune
Ya kalleta har xaiyi magana saiya fasa ya nufi part 'din LABEEBAH
Ganinta yayi a falo tanata taya SAUBAN wasa
Ta kalleshi ya sakar mata Murmushi ta mayar mishi
Ya qaraso da xama kusa da ita Yace am sorry nutsuwata Wlhi XARAH CE Tace tana da tsoro wai bata iya kwana ita 'daya bah shiyasa baki ganni ba
Shuru LABEEBAH tayi dan axahiri itace matsoraciya mejin tsoro ba XARAH bah Amma meyasa Tace mishi tanajin tsoro.
Ganin tayi shuru yasashi cewa dan Allah kiyi.........
Bata bari ya qarasa ba Tace ina kwana da fatan kuntashi lafiya

Yace lafiya lau Amma baxan qara kar6ar wannan gaisuwar ba. Dan ba ita nake buqata bah Tace toh wacce kake buqata
Ya kama fuskarta ya manna mata kiss a goshi da hanci da baki Yace xaki iya rungumata kiyi min kamar yanda namiki yanxu plx kar kice Komai
Tace bin umarninka shine numfashina
Karka damu xamma yanda kakeso
Nagode sosai
Tace ya kwanan XARAH.
Ananne ya Sosa qeya ka'dan yace lafiya
Tace haka akeso ga breakfast can Momy ta aiko tun'daxo
Ya 'dan waro ido da kallan agogo Yace kai ya akayi lokaci ya qure haka.
Sai yanxu takaicinsa ya kamata Tace gaskiyane ka huta da yawa shiyasa lokaci ya maka baxata

Tashi yayi yana cewa aransa yarinyar nan neman magana take
Amma afili cewa yayi toh muje kiban mana

Tace toh bara in kira XARAH ko
Yace no bari na kirata
Yafa'da da  sake SAUBAN wanda tun shigowar shi ya maqale mai

Toh LABEEBAH Tace mai kawai da binshi da kallo

Yana komawa falan XARAH ya ganta tana kuka wiwi
Cikin tashin hankali yayi kanta da tambayar lafiya Tace watoh dan LABEEBAH tafini darajah agunka shine ina ambatarta kayi gunta
YUSUF ya dafe kai
Yace toh yi hakuri ba haka bane ke da LABEEBAH 'dayane aguna plx Ki fahimceni
Cigaba  tayi da kukanta. Ya rungumeta yana lallashinta
Can dai tayi shuru tana sauke ajiyar xuciya
Yace Yauwa.tashi toh muje muyi breakfast

Tace nidai saidai kaxauna anan in kawo mana Komai nan
Bayanda YUSUF xaiyi sai gya'da mata kai da yayi ta ficce
Direct part 'din LABEEBAH tayi suka gaisa Sannan ta tambayeta breakfast 'din
Tace yana can falan
XARAH tayi Murmushi Tace gaskiya hankalina yayi gunki banda haka yaci ace naci karo da shi kafin in qaraso nan
LABEEBAH ma tayi murmushin Tace Hakkane Amma me yasami fuskarki kamar kinyi kuka
Tace haka  kawai natashi da ciwan ido ina addu'ar Allah yasa karnah xama ke
Tace ayya sannu ciwan ido ba da'di
Tace ina xuwa
Tace toh
SAUBAN wasanshi yake Sam be waniyi 'daukin Ganin maman nashi XARAH ba

Kamar ance LABEEBAH leqa Babban falo aiko Tatashi ta leqa nan taga ba YUSUF ba dalilinsa haka ba XARAH da abincin da tajera
Tadawo ahankali tana tunanin wai me yake shirin faruwa ne
can dai ta'daga kafa'da takori tunanin xuciyar tata

Abinda yabata mamaki shine yanda taga YUSUF da XARAH sun fitoh Suna dariya da kagansu kaga Masoya YUSUF ya kama hannun XARAH batasan me yake CE mataba ya shige mota ta 'dagamai hannu ya ficce
Saita XARAH Koma part 'dinta

Shuru LABEEBAH tayi kawai taqi 'dauke idanta a window dan tafa'da wani birkitaccen tunani

Da yamma ne LABEEBAH tana kitchen tana ha'da musu abinci dan taga Komai na buqata a kitchen 'din akwai harsu nama kifi gasunan a refrigerator shi yasata San yin girkin. Kuma takira Momy Tace karta turo musu da Komai sai kayan gwari

Aiko taturo musu harda Su kayan Qamshi

XARAH ta shigo kitchen 'din tana qare mishi kallo Komai yayi daidai saikace yaran sarauta ko 'yayan shugaban qasa.
Tace wow gaskiyane kitchen din yayi kyau
LABEEBAH Tace eh Momy tayi qoqari Allah ya biyata Tace AmEEn
Bara natayaki
Nan sukayi girkinsu me da'di da rai da lafiya. sukaci

Wajan 6:00pm YUSUF ya shigo gidan.
Tabbas part 'din LABEEBAH yayi niyar shiga duk dako ya dawo da buqatar San Ganin XARAH Saidai me😳

Yana fitowa daga motar XARAH tafitoh tariqe mai hannu Tace Wlcm my luv da fatan kadawo lafiya
Farin ciki ya cika xuciyar YUSUF musamman data Sha wankan Riga da wando tayi kyau sosai kamar ya sataceta ya gudu
Yakai bakinsa Cikin nata ya tsotsa ka'dan kana yajata part 'dinta
Anan suka baje suka fara aikawa junansu sakwanni luvvvvv

Hawaye ne ya xubuma LABEEBAH sharr
Dan tana xaune kan kujerar da take kallan windan farfajiyar gidan
Tana kallan dawowar YUSUF da kissing 'din daya yima XARAH

Share hawayanta taji anayi. Takalli SAUBAN daya xage yana goge mata hawayan
Yace momyna kidena kuka banaso kinji
Tayi Murmushi Tace ban san lokacin da nayi shiba SAUBAN Amma karka damu baxan qaraba kaji
Yace toh

Tunanin da LABEEBAH tayi 'dayane shine YUSUF xaiyi kwana bakwai a'dakin XARAH qila ya biyema XARAH hakanne dan karya shiga hakkinta
Idanko Hakkane mexaisa tadamu gwara tabarsu sukagama kwana bakwai 'dinsu yadawo gareta

Qarfe takwas na safe LABEEBAH tagama Komai
Farfesun naman ragone tayi Sannan tayi musu ha'din tia wanda yasha kayan qamshi
Ta yaba aikin Momy sosai dan duk abin buqata ta saka musu cikin kitchen 'din

Saita gasa buredi da kwai ajiki
Tajera musu a dining kana ta ibi nasu ita da SAUBAN sukayi falanta.

XARAH da YUSUF suka fitoh sukayi breakfast 'din

YUSUF Yace Amma fah yayi da'di farfesun nan
Tace eh aitana qoqari LABEEBAH
Gaban YUSUF yafa'di Wlhi shi Sam mantawa yake da LABEEBAH in yana tare da XARAH Bala'i😳

Yayi shuru da  tsayawa dayin Komai
XARAH Tace lafiya Yace nayi tunanin Momy CE ta aiko dashi
Tace ai LABEEBAN CE tace karta aiko dashi dan xamu dinga bata wahala ne kawai
Tashi yayi Yace yayi kyau nixan ficce
Tace muje in rakaka
Hakako suka fitoh hannunsu saqale da juna
ya shige motarsa
LABEEBAH na kallansu  ta falanta XARAH tamanna mishi kiss💋 yajah motarsa ya ficce.
wani masefaffan kishi ne ya caki xuciyar LABEEBAH
Hankalinta yatashi
Bata ankareba XARAH tashigo falan nata
Tace kiyi hakuri banxo na tayaki aiki bah Wlhi.....
LABEEBAH ta katseta da cewa ina kwana
Tace lafiya da fatan kuntashi lafiya
Qalau LABEEBAH Tace sai sukayi shuru duk kansu.
Ita LABEEBAH game takeyi a wayarta itako XARAH shuru kawai tayi tana kallan SAUBAN da yake wasansa Wanda kallo 'daya yamata ya 'dauke fuskarsa
Tace SAUBAN kaba ganni bane
Abinka da yaro saiya kalleta Yace naganki mana Momy
Tace shine baxa kamin oyoyo bah
Yace aikema bakyayimin in kika ganni momyna nace me mun yafa'di hakan da nuna LABEEBAH.
Lokaci 'daya kuma yabi boll 'dinsa yaci gaba da wasanshi

LABEEBAH najinsu. Saitaji bataji da'din hakan bah
Takalli XARAH ka'dan Tace mexai hana ki  ware lokaci kidinga bah SAUBAN kulawa saboda halin rayuwa
Tata6e baki Tace banda wannan lokacin
Bawai kuma nadamu da abinda ya faru yanxu bane
Kinsan dai Ni yara ba damuwa nayi dasuba
LABEEBAH Tace ko
Tace da gaske mana
Ke bakiga hakan bah
Tashi LABEEBAH tayi Tace nada'de da gane hakan
Bara nayi wanke wanke nasan kungama ko
XARAN ma tashi tayi Tace eh tun'daxo. Muje in tayaki

Suna cikin wanke wanken ne Hajjiya Turai tasawo kanta Babban falan nasu tana ko'da sallama
XARAH tafita da gudu ta rungumeta tana cewa nayi missing 'dinki xauna kisha labari

Turai taxauna XARAH taxauna daf da ita Tace kan ubah haka maganinnan yake da aiki.
Wlhi bakiga yanda ya gigita YUSUF bah. Gaskiyane maganin mata shine mace agun 'da namiji bala'i
Turai tasheqe da dariya Tace angaya miki wannan magungunan na wasane.
XARAH tace gaskiyane nayarda ba nawasa bane
Turai tace Yanxu mah wasu nakawo miki dan yafi wancan aiki. Amma fah da ku'di
XARAH Tace Kinsan banda matsala dasu bani kawai nagani
Turai tayi Murmushi da cewa ina shegiyar taki.......
Saurin waro ido XARAH tayi tana leqa kitchen cikin tsoro takama hannun Turai cikin murya qasa qasa Tace tana cikin kitchen
Turai tayi qasa da murya Tace kai habah
Tace Wlhi Kinsan na manta da ita nafitoh inata baragada
Turai tajah tah part dita tana cewa kemadai Wlhi sai ahankali yaxaki saki baki haka ninayi tunanin tana part 'dinta ne
Tace tana kitchen Amma ina ganin bataji bah
Nan Turai tabaje mata harka Wanda XARAH tafara cilla ido tana ta6awa

Shuru LABEEBAH tayi. tabbas taji abunda suke cewa kuma tagane abunda suke nufi
Itama tunda taga Hajjiya Turai taji ta tsaneta kuma dama tana ganin sauyi agun XARAH tuncan baya
Yanxu tafara xargin tana tusama XARAH wasu halaye
Shuru tayi can da taga tsayuwar tata bata da amfani saita 'dauraye hannunta tasaka aranta yanxu xata fara bin tunaninsu

Yau kwana bakwai kenan
☺☺☺☺
Haka ko ya faru dan LABEEBAH tagano bakin xaran manufarsu akanta
Abinda yabata mamaki yasata kuka shine yanda XARAH takasance haka. Tayi sabo da hu'dubobin Turai
Sam sai yanxu tagane XARAN data sani da ba itace yanxu bah
Wato ayanxu duk xamanta da XARAH raina mata hankali kawai takeyi

Meyasa Ni LABEEBAH ban gano hakan tunda wiri ba
Meyasa kikamin baxata XARAH
Saiga hawaye ya wanke mata fuska tana tuna hirar da taji sunayi jiya inda taji XARAH nacewa har abada YUSUF natane ta 'dan'dani xumarsa kuma baxata ta6a bari wata 'ya mace tasanshi bah
Dan xata toshe kowace 'kofah yanda ba wata sai ita agaban YUSUF
Turai Tace shegiya LABEEBAH dai taxama hoto
XARAH tayi dariya Tace aida hotoce da Sauqi tunda xa'a dinga kallanta. Kango xata xama Wlhi

ba photo bah
Turai Tace yaudai Karki manta kwananta ne dan kin cika kwana bakwai 'dinki yau
XARAH Tace Lalle naga alamar bakya 'daukar karatun nawa.

LABEEBAH ta share hawayanta dan kammala tuno wannan furucin nasu Tace namiji ya ha'damu XARAH idan najure wata ranah ina tsoran ranar da xankasa kasa jurewa hakan

Da YUSUF  ya dawo XARAH fitowa tayi ta tareshi suka yi part 'dinta
Duk da LABEEBAH taji furucin XARAH akan baxata bari YUSUF yaxo gareta bah
Amma tayi mamakin yanda yau ya kasance kwananta Amma YUSUF baibi ta kantabah
Yau kusan kwananta hu'du rabanta dashi Amma ko ajikinsa

Shuru shuru har kusan goma 10:00pm YUSUF baixo gareta bah
Sai tajah musu bargo ita SAUBAN suka kwanta abinsu

Haka Washe gari tagama Komai tajera musu ba kunya suka fitoh suka cika cikinsu XARAH ta rakashi mota
Sannan tayo part 'din LABEEBAH suka gaisa LABEEBAH sai binta take da kallo tana mamakinta
Amma XARAH tayi tamkar batasan kallanta takebah saima tashi da tayi
Tace ina jin bacci dan jiya ban samu yiba bari naje nakwanta kibarmin wanke wanken Xanyi
Tana fa'din haka tayi part 'dinta bata jira cewar LABEEBAN bah

LABEEBAH tasaki baki sakaka 😼
Can Tace mutum kenan ashe ba abinda yafi mutum saurin canjawa lokaci 'daya
Itadai ko amafarki akace mata XARAH xatayi mata wannan budulcin baxata ta6a yarda ba bare a baiyane

Abun fah haka yaci ga da tafiya
XARAH qememe tamantar da YUSUF wata LABEEBAH
Yau watansu uku

Watan Farko ciwan cikin marar LABEEBAH ya tashi mata cikin dare aiko Allah ya temake ta taxo da maganin da Ya Usman yabata watan bikinsu
nan tajiqa tasha
Allah ya temaka bai wahalar da ita ba
Haka wata na biyu tana cikin kitchen  ciwan ya tasar mata lokacin tare da XARAH a kitchen 'din
Dan haka tayi saurin  jiqa mata tasha maganin tabata tasha
Toh wannan watanne tayi amfani da maganin gabaki 'daya
Hankalinta ko yatashi tunaninta wani watan yaxatayi dan Ya Usman Yace mata me bada

maganin har yanxu bai dawo garin na kano bah
Amma yaje gun wani ya kar6o mata Allah yasa adace kamar wancan xaixo da kansa Abujan ya kawo mata
Tace toh ya tawo mata da Aunty Rukayya da Sumayya toh kawai Yace mata Amma daya tashi xuwa shika'dai yaje mata

Ayanxu dai saidai LABEEBAH ta dafah ma YUSUF da XARAH abinci sulamishe Wato sun maida ita 'Yar aiki

I xuwa yanxu LABEEBAH tagane Komai da Komai
Yau tayi al'kawarin xata yimah XARAH magana.

Dan haka Bayan ta idar da sallar La'asar dayin laximinta da addu'o'inta dama tayi wankanta taci Riga da siket na material tayi kyau aciki sosai dan kayan sun ka6eta
Sai tanufi part 'din XARAN
Aiko tasameta tana waya dagaji Kasan da mijinta takeyi Tace OK yanxu kana hanya tanaji YUSUF Yace eh Tace toh sai kaxo takashe wayan da kallan LABEEBAH Tace in aka ganki da magana nasan mungama abinci bare kice kinxo tambayar mexa mudafa
LABEEBAH taqara jinjina rainin hankali irin na XARAH tare dajin wani tsanarta
(Kishi kenan mesa mutum manta mutunci bare adalci)

.
[8:44PM, 08/10/2016] Rahamat Nalele💋:

Tace ba wannan bane ya kawoni

Ke 'yar uwatace XARAH
Baidace aji kanmu bah

Ban san yaushe bane ha'kurina ya gaxa 'daukar wannan

Naxo ne in roqeki kitsaya akan hakkinki kawai. kidena shiga nawa
Naga la'amar kin manta cewa mu biyune Matan YUSUF acikin gidan
Xaqewarki tayi yawa
Koda da ballagaxa kike xaune da ita matsayin abokiyar xamanki yaci ace kinji tausayinta kin bata mijinta.

Ban San da'din maxa bah adaaaaa
Dan ban damu da in sani bah
Shiya yasa nabar miki YUSUF tunda nalura kinsan ya da'dinsu yake
Shiyasa namiki uxiri nabarki ba wata 'daya ba. Ba biyu ba. har uku
Nasan yanxu inba San xuciya bah kin lashi xumar YUSUF har kin saba da ita

na roqeki kibarni da Mijina haka

Baxan iya tauye miki kwananki bah. Amma baxan iya bar miki nawa yanxu bah

XARAH XARAH XARAH nakira Ki sau uku
A yanxu inasan inji da'din maza
Maza ba
Inji ya suke
Ya akejin su
Sannan
ya abin yake

Atakaice yau ina buqatar Mijina
Na roqeki da Allah karkisa mukai matsayin daxa muyi abunda xa'aje akaimu gaba.

LABEEBAH CE mai wannan furucin ga XARAH

🤔

Afurgice XARAH Tatashi takalli LABEEBAH
Tab gaskiyane takaita mu'kura tasan LABEEBAH tana mata kawaici akan Komai
Saidai itadai baxata iya yi mata kawaici akan YUSUF bah
Kuma al'awari tayima kanta ita ka'daice da YUSUF
Dan haka takalli LABEEBAH a wulaqance cikin raini Tace meyasa kikayi gangancin Auran
Wanda xuciyata take so
Akan MASEEFAR dana afka ta MASEEFAR SOO Xan iya yimiki abinda yafi haka mah
YUSUF nawane Ni 'daya
Ina sanshi kuma baxan bari wata mace tara6e shiba.

Me kike nemah me kika sani akan maxa da xakixo kina magana akan nabar miki mijinki
Wlhi ko yanxu isata CE tasa YUSUF maqale mun
Namantar da shi kowace mace
ba wacce xaigani agabansa saini
Ina baki shawara LABEEBAH kifita daga harkar YUSUF dan yanxu yafi qarfinki .....

Ta numfasa ha'de da dariya kana taci gaba

kin iya rasa KAMAL kuma kikayi hakuri akan wane dalili xaki damu da YUSUF meyasa........

Kinga malama da kata magace kinyi akan baxaki barni da YUSUF bah saboda nake ne ke 'daya
Hmmm ba shakka kinkai nan gurin

Bada abinda kika fini XARAH saima abubuwan da nafiki dasu wajan 'daukar hankalin maxa
Kina wani cewa isarki CE tasa YUSUF maqale miki ni koba maganin mata saina koya miki hankali kirubuta ki'aji
Kinyi furucin yafi qarfina ko. Nikuma saina nuna miki nice nafi qarfinsa daga shi harke
Tana fa'din haka tayo waje
Tafito kenan YUSUF yana sawo kan motarsa
Baqamin bugawa gabansa yayi bah da ganin LABEEBAH bah.
Shidai ya rasa abinda yake damunsa akanta
Sam mantawa yake da ita arayuwarsa
Part 'dinta tayi takama hannun SAUBAN Tace xomuje unguwa
Yace yauwa momyna
Nan taxaro gyalanta ta tajanyo kofar ko kullewa batayi bah tayi hanyar waje

Da sauri YUSUF yafitoh daga motarsa yasha gabanta
Tare da dur'kusawa aganta Yace dan Allah dan Annabi kiyafemin Wlhi bansan meyake damuna bah
Tace ko
Yace Yah
Wlhi dagaske
Tace koma me yake damunka kai kasani dan Allah tashi kada wani yaxo yaganka yayi tunanin wani abu
Tashi yayi jikinsa asanyaye
Yace ina xaki
Tace inda nayi niya.
Yace kin tambayeni ne
Tace akanme xan tambayeka mijinane kai
Yace plx nutsuwata....
Karmiyi haka dake
Kisani duk matar da tafita unguwa batare da sanin mijinta bah tsinuwar Allah ta tabbata akanta
Dan duk wani taku 'daya idan tayi Mala'iku tsine mata sukeyi
Tace Au yanxu ne Kasan da cewa ni matarka ce
Yace tunda aka 'dauramin Aure dake nasan ke matata CE

Xatayi magana ya katseta da cewa kitemaken dan Allah kiyafemin
sannan Nayarda da duk inda xaki amma Ni xan kaiki
Tayi Murmushi dan ganin XARAH tafitoh daga part 'dinta
Tace toh muje kakaini

Har xasu shiga motar XARAH Tace my luv ya daga xuwa sai fitta Bayan Kasan tun safe nake da muradinga San kasan cewa ajikinka
YUSUF ya kalli LABEEBAH yaga tayi fuska yamaida kallansa ga XARAH nan ya hango rikicin so kala kala kamar yanda shima yadawo dasu
Yace ki'dan min afuwa nakai LABEEBAH unguwa nadawo
Tace buqatata tafi tata mahimmanci

LABEEBAH talalleshi Tace kaga Malam je ka biya mata buqatarta dama fah munsan hanya Tafa'da dasan ficce
Yaqara shan gabanta
Nan taga tashin hankali a idansa kamar xai mata kuka Yace plx Ki temaken dan Allah
Shuru LABEEBAH tayi hawaye ya xubu mata saijin hannunshi tayi kan kumatun nata yana goge mata
Kallansa tayi taga shima hawayanne ya xubu mishi. Ganin haka yasata juyawa  tayi part 'dinta tana hawaye
Sauke ajiyar xuciya YUSUF yayi da runtse idansa ya sauke akan SAUBAN Wanda yayi shuru yana kallansa Yace Dady kasaka momyna kuka metayi mah
YUSUF ya rage tsawansa ya kama hannun SAUBAN Yace batajin da'dine my boy  jeka lallasheta kace ina xuwa kaji
SAUBAN Yace toh meyasa kaima kayi kuka. Yace saboda banasan kukanta ne maxa jeka kaji
Aiko da gudu SAUBAN yayi part 'din LABEEBAH yana kiran momyna momyna

XARAH tata6e baki Tace kar lamarin LABEEBAH ya dameka xo muje kasha milk me sanyi Wanda xai kwantar maka da hankali
Kallanta YUSUF yayi Yace inajin ina aikata ba dai dai ba.
Tace koma miye kaxo muje kahuta saimu fuskanci mafuta
Haka yayi part 'din XARAH
Duk abinda tasan xatayi ta'dauke tunanin shi akan LABEEBAH shi tayi
Kuma taci galaba dan LABEEBAH tanajin futarsa Sallah ko kallan shashinta baiyiba

Kan ya dawo ne XARAH tashiga tunanin wane hukunne ya dace da LABEEBAH
Saiji tayi wayanta na ringing
Jameel tabani ta'dauka
Yace Kinga nacanjah tunani baxan iya jure har sai shekara tayi xan mallaki LABEEBAH bah
Na baki kwana uku kiyi abunda xaisa ya saketa inba hakaba mufuskanci matsala

Cikin fusata XARAH Tace ai Kasan igiyar Auranta a guna take daxaka bani kwana uku
So kake inje ince  masa saketa kuma ya saketa

Yace Lalle XARAH bakisan Waye nibah
Amma namiki magana tun muna mu biyu kije kibi hanyar da kikabi kikayi makircinki kika sami YUSUF yanda kikeso.
Toh wannan Hanyar nakeso kibi kisaka ya saketa. Kwana uku nabaki Wlhi
kikayi gigin in aikata hakan Wlhi saikin nemi Auran Ki kinrasa
Dan YUSUF sai yasan Komai akan yanda kika sameshi
Yana fa'din hakan ya kashe wayansa
Yayinda hankalin XARAH yatashi nan takira Hajjiya Turai tagaya mata Komai
Tace dallah bar 'dan iska
Ki saka Su Musa jage Su kau miki da 'dan iska
Aiko nan take takira wa 'yanda suka satoh mata KAMAL alokacin baya Tace tanasan Su kashe mata Jameel xuwa gobe su ha'du a gidan Turai taga pix hota kisan

Sukace angama ranki ya da'de Amma sai gobe Komai xai wakana
Tace ba matsala

Tana sauke wayan YUSUF na shigowa
Taje ta rungumeshi suka fara ya mutsa juna

Washe gari XARAH Tacema YUSUF xata gidan qawarta plx suje ya sauketa adawowar shi ya biyo ya 'dauketa Yace toh

Sun fitoh danyin breakfast sukaga dining wayan ba Komai🙅🏼

YUSUF Yace ya haka
XARAH tacije yatsa Tace bara in shiga kitchen yanxu in ha'da maka
Yace OK
Tanayin kitchen ya tsinci kansa dayin part 'din LABEEBAH
Bayan ya shiga falan saiya kulle 'kofar falan harda key
[8:55AM, 09/10/2016] Rahamat Nalele💋: LABEEBAH na kallansa ya qaraso gareta
Nan yaga soyayyan dankali da egg ha'de da kakkauran tia suna karyawa ita da SAUBAN abinsu
Ya xauna dab da ita   Yace ina kwana
Takalleshi ka'dan aciki Tace lafiya
Yayi Murmushi
Yace xan samun turare dan Allah
Ta kalleshi sosai Tace mexai hana
Yace Yauwa toh tashi Kiban
Tayi shuru dan baxa taso Tatashi a haka bah
Dan kayan da tasaka shegun kayane
Riga da wandone sun matseta tsam
Komai nata ya baiyana.......
Yakatse mata tunaninta da cewa tashi mana yaqare dabin surarta da kallo
Tashi tayi ahankali tayi bet room
Aiko yabita
Saiji tayi an rungumeta ta baya
Batada buqatar sanin waya mata hakan tasan sai mijin nata
Nan tafara kici kicin kwatar kanta
Ya riqeta tsam yafara magana cikin sanyayyiyar murya.
Yace plx nutsuwata Ki fahimceni Wlhi bansan me yake damuna bah kiya femin
Saita fashe mishi da kuka mecin rai
Dama yasan kan abinsa
Dan haka ya juyo da ita gabansa ya rungumeta tsam yana shafah bayanta alamar lallashi
Nan tayi shuru
Yasami yanda yakeso dan haka ya kwantar da ita kan gado ya hau kissing 'dinta tako ta ina

Yanda ya rikice mata shi kadai yasata tausayinsa
Tana jinshi yana qoqarin cire mata riga tabarshi saidai da taji yafara tsotsarta tayi yunqurin kwatar kanta ya 'dago da kansa ya dire afuskarta yace karki hanani abinda yadace nayishi tuntuni

tureshi tayi hawaye na xubar mata Tace Nina yafe maka Amma na roqeka kabarni haka...
Yace rayuwar baxata ta6a tafiya ahaka bah plx kibarni
Share hawayanta tayi tatashi da kallanshi Tace xakayi breakfast ne
Ya harareta Yace saidai luv... Breakfast
Xatayi magana wayanshi tafara ringing
Bakuwar number CE ya 'dauka da hello
Sai yaji abokin Yayansa Jameel ne
Yace mai yanasan Su ha'du yanxu a office 'dinsa akwai gaggarumar maganar daxai gayamai
YUSUF Yace toh insha Allah xaka ganni yanxu
Yace Yauwa
LABEEBAH Ta kama hannunsa suka fitoh falo
Annan ta ha'da mishi Komai tabashi
Aiko ya cika cikinsa dam
Sanman Yace mata xaikai XARAH unguwa yana sauketa zai dawo
Toh LABEEBAH Tace masa dan tasan ba dawowa xaiyi bah.
Kuma yau tasaka aranta saita kwana da mijinta ko sama da qasa xata ha'de
Har 'kofar falan XARAH ta rakashi ya manna mata kiss Yace ina sanki
Tace nima haka
Sannan takwaci kanta tayi shashinta

Komai XARAH ta shirya mishi tana dai xaman jiransa ne dan taci nata
Tunaninta waje ya fita shiyasa daya shigo tatareshi da murna tana cewa na gama ha'dama
Komai Yace lokaci yatafi muje kawai Tace bakaci Komai bah xamu tafi. Yace naci gun LABEEBAH
Tace dama can kaje Yace eh
Saitayi shuru
Yagane bataji da'din hakan bah. Sai ya yafah mata gyalanta da kama hannunta suka ficce

Har ya sauketa agidan Hajjiya Turai tashiga gidan bata kula shibah yayi Murmushi yajah motarsa
Direct asibity yayi bayan yakai
office 'din Jameel ya nufa
Anan ya ganshi tanata safah da marwa
Yace lafiya Ya Jameel
Hawaye ya xuboma Jameel Yace na cuci Kaina YUSUF naci amanar KAMAL na yau dareshi na biyema she'daniyar matarsa
YUSUF Yace duk meyasa haka yafaru
Yace kafin in fara baka labari inasan kaya femin
YUSUF Yace bakamin Komai bah mexaisa na yafe maka

Kuka sosai Jameel yafashe dashi dan tuna 'daxo da safe daya fitoh dan Xuwa office 'dinsa daqer yasha ahannun Su musa jage
Dan qiri qiri yaga mutuwa Allah ya temakeshi yasha ahannunsun.....

YUSUF Yace plx Jameel kasa hankalina yafara tashi meya farune

Gyara xama Jameel yayi ya kwashe duk abinda XARAH tayi dan ta mallake shi matsayin mijinta

Ihu YUSUF yasake lokacin dayaji XARAH CE ta kashe Yayansa KAMAL
Idanshi ya fara juyewa
Hankalinsa ya tashi
Ya bala'in furgicewa da lamarin XARAH
Ya tashi afurgicen
Tare da kama kansa
Ya fashe da wani gigitaccen kuka
Wanda kallo 'daya xakama YUSUF kaji kana san tayashi kukan
Yana kuka Jameel na kuka
Sun 6ata lokaci ahaka

YUSUF yafara tafiya cikin layi
Jameel yayi 'ko'karin San rigeshi
YUSUF ya 'dagamai hannu Yace karka ta6ani
Yana fa'din hakan yayi waje. Jameel ya bishi da kallo

Shiga motashi yayi hankalin shi na neman gushewa
Ayanda ya figi motar ka'dai ya isa ya tabbatar maka da cewa bame hankali bane ya figi motar

Tuqi YUSUF yake yi ahaukace
Dan kowa kauce mishi yakeyi dan Tsira da ransa
Ahaka ya iso gida dayima megadi wani kira cikin muyar buqatar temako
Da sauri ko megadi ya bu'de mai. Dabadan megadin yayi saurin kauce mai bah daya begeshi
YUSUF yayi parking Amma yakasa fitowa dan jin yanda girjinsa yake mishi xafi
Ba shakka yaji  wani ciwo ya caf Ki xuciyarsa  yayi saurin dafe girjinsa yana hawaye

Aman jini ya fara yi
Yana cikin wannan halin ya danna numbar XARAH ya kirata
Xuciyarshi tacika fam da tsanarta

Tace toh yaran Momy gobe da safe direba xaixo ya kwasheku ya kaiku garin na Abuja dan tana ha'da wani walima bayyanar abinda basuyi xatoba dan haka tanasan ganinku agun LABEEBAH da XARAH sukace toh
Duk da Innah talura yaran nata na cikin damuwa Amma batayi gigin tambayarsu bah
Dan tasan ko tace miye cewa xasuyi ba Komai
Mu samman ma XARAH da jiya tana kallanta cikin dare tana riskar kuka dan a 'dakinta suka kwana BABAH yaje qauyan garin babba nanan kano wajan wani amininsa acan ya kwana

Tajuya ta fitta
Sumayya takwashe da dariya Tace ai xuwa Abuja danine

Rukayya Tace hmm bakiga mutanan naki duk Suna cikin damuwa bane
Sumayya Tace eh nagani ai nadena damuwa da damuwarsu tunda sun xa6i subarta acikinsu ai shikenan

LABEEBAH taja numfashi tayi shaha'da ta kunna wayar tata
Aiko ko 2 minutes batayi bah saiga wayan KAMAL aljanin nata ya shigo
Aiko saita rushe da kuka kowa ya xuba mata ido tayi saurin shanye kukan ta'dauka da cewa hello
Yace waya ta6amin babyna
Taturo baki kamar tana gabansa Tace kaine mana
Dan Allah a ina kata6a jin anyi Aure tsakanin aljani da mutum

Murmushi KAMAL yayi Yana kwance akan gadan shi
Marwan na kujera yana kallan wani film na mutuniyar tawa Rahama Sadau👯 waishi JININ JIKINA😄.

Yace toh ya xanyi Babyna Allah ya jarab ceni da MASEEFAR SONKI. Akaina xa'afara wannan Auran

LABEEBAH tagyara muryar xatayi kuka
Yace Kinsan Allah kika yimin kuka alokacinnan da nake buqatar farin ciki
Saina 6ullo miki yanxu na maqureki da tsotsan wannan munafukin bakin nan  naki daya ke cewa wayyo aljanina kaxo gareni naxaqu inganka  axuci Amma baki yana cewa dan Allah karabu dani
Hakane ko ba haka bah. Yafa'da tasan tabashi amsa
LABEEBAH takalli Su XARAH da suka xuba mata na mujiya (ido) ta marairaice Tace ba haka bane fah😳
_ba haka bane fah_
Ya maimaita mata furucin nata da cewa xaki fa'damin gaskiya ko saina 6ullo yanxu.......

Tayi saurin cewa hakane da fashemai da kuka Yace ya salam
Cikin shashsheqa Tace dan Allah karka 6ullo nayi shuru
Yace ai ina kallanki goge hawayan ko na goge miki
Da sauri tagoge hawayan Tace toh nagoge
Yace nayi missing 'dinki babyna xanji da'din ganinki gobe
Tace a ina xaka ganni
Yace ba naja xakuxo abuja bah
LABEEBAH tawaro ido Tace harcan xaka Bini
Yace mexai hanani binki Bayan mu iska kawai muke Bi. Kanki qifta ido munje bangwan duniya

fah😝

LABEEBAH tajah numfashi. Tace hmm ina sanka
Yace nasani Babyna kici gaba da suna kinji
Ta 'dagamai kai kamar yana gabanta Tace toh

Kiss💋 ya sakar mata tare da kashe wayan
Marwan Yace naga alamar kanajin da'din jin kukan Auntyna
KAMAL Yace haka take
Sam in batayi bah. hankalinta baya kwantawa
Amma kukan yana tafarfasa xuciyata

Marwan Yace toh kadena sata mana
Yace ko ban sata bah sai tasa kanta

LABEEBAH ko na ajiye waya tayi shuru kawai tafa'da tunani
XARAH Tace hmm da aljanin kikayi waya
LABEEBAH ta kalleta Tace eh
XARAH tayi murmushin yaqe dayin shuru
Sumayya tayi Murmushi Tace kudai bakwa rabo da matsala
Wannan na fitta daga nan wancan xata 'dauka
Rukayya tace kiji wai aljani
Ke yanxu da aljani kike soyayya
LABEEBAH Tace eh
atare Rukayya da Sumayya sukayi dariya
Rukayya Tace wannan ai story ne.
Sumayya Tace babbama kuwa

Shuru LABEEBAH tayi musu da Qara kashe wayanta.

Washe gari tun qarfe tara direba yaxo ya kwashi LABEEBAH da XARAH Sumayya xuwa garin na Abuja

A gajiye suka Isa
murna tacika Momy Safna da Sagna Dady
Kowa yayi murna da xuwansu
Hajjiya Zainab matar Alhaji Nasir qani ga Dadynsu KAMAL tadinga yaba LABEEBAH da XARAH tana masha Allah
Kakah mah tayi murna Sosai da ganinsu

Bayan sun huta sunci sun sha LABEEBAH Tace hmm nagaji bari na'dan kwanta
Sumayya tayi gunsu Sagna
XARAH ko xagawa tayi Bayan gidan tana buqatar ka'daicewa......
Saidai me😳

Tana xuwa tahangi KAMAL da Marwan Suna hira cikin nisha'di
Gabanta ya tsinke ya fa'di. Nan nutsuwa tabayyana agareta
Hawaye ya xubo mata
Tabbas KAMAL ne wannan dan tatabbatar ma kanta shine tun ganin da tamasa a kano
Aiko tarushe da kuka wiwi
KAMAL ya kalleta ka'dan. Shiko Marwan xuba mata ido yayi kawai xuciyarsa tatafi tunaninta
Ya rinya kyakkyawa da ita gata kalan tausayi Amma ta aikata wannan aika aikam
Bai Ankareba ya ganta durqushe gaban KAMAL tana wani kuka me ban tausayi Tace nayi nadama nayi dana sani nayi Allah wadai da rayuwata nayi asarar da har in mutu baxan maida itaba
Na sani Kai KAMAL ne
Dan Allah dan Annabi karufamin asiri Karki tona wannan abin Allah wadai dana aikata maka.......
Ta qarashe da rushewa da kuka
Wani abune ya muntsini xuciyar KAMAL Wanda ya Haifar mai da tausayinta
Sai kawai ya tashi ya bar gun
Taqara rushewa da kuka
Marwan bai 'dauke idansa akantaba yayi Murmushi Yace XARAH ko
Ta kalleshi ka'dan tare da 'dauke kallan nata tacigaba da kukanta Yace Kinga malama baxafah Ki takuramin bah
Ki tashi kibar nan dan Allah
inajin kukanki har cikin xuciyata
Plx dan Allah temakeni kibar nan gurin
XARAH tatashi da jifan shi da harara Tace baxan bari bah kai katashi mana
A rayuwar Marwan yana San mace me tsiwa da rawar kai
Shiyasa Sagna tayi saurin shiga xuciyarsa. Wannan ra'ayinsa kenan
Yayi Murmushi Yace wow gaskiya ne in bakiyi tsiwa bah a tambayeki
Irin wannan harara haka. Kinga bacewa nayi ina sanki ba. Daxa kimin hararar Masoya
Ya ta6e baki ka'dan yaci gaba da cewa Kumama ni matsoracine koda kin soni aranki baxan aureki bah. Dan ina tsoran kar na Aureki wata ranah kiga qanina Ki kashe ni kice shi kikeso ..........

Tun da ya fara magana XARAH tasaki baki da hanci ido tana kallansa da mamakinsa
Akanme daga ganinta xai mata sharrin tana sanshi daga harara saiya juya mata manufah
Lokacin da yaxo furucinsa naqarshe abin ya 'kona xuciyarta tafashe da kuka me ban tausayi
Ya kalleta ka'dan da murmushin mugunta ha'de da tausayinta Yace am sorry......

Tafiya tafarayi tana cigaba da kukanta
Yace na'danji sanki ka'dan
Tajuyo ahankali takallesa sai taga ba ita yake kallo ba wata fulawa yake kallo.
Ya juyo ahankali ya kalleta Yace ina san Sagna Sannan ina 'dan sonki shin ya ha'din xai kasance
Cikin fusata XARAH taqara kai mishi harara Tace bana sanka bana sanka bana sanka
Yace da gaske naji sanki ka'dan. Amma Wlhi soyayyar da nakema Sagna taninka taki so dubu.

Kina wani maganar baki sona keyanxu idan da xa'aji abinda kika aikata waxai aureki da wannan mummunar xuciyar taki. wacce Sam ba Allah acikinta. Wlhi tausayinki naji kuma nasan baxa kiqi na'am da soyayyata ba. Saidai kitsaya wani alaye. Gashi kuma inda xakiyin baxai ta6a tasiri ba. kawai ki share dan nima qarfin hali nayi kawai nayi dan nasan da wahala na Aureki bakiyi min abinda kikama yayanah KAMAL bah

XARAH takece da wani kuka Tace natsaneka
Tana fa'din hakan tafice daga gun
Marwan yayi Murmushi yace story kenan. banji sanki bah XARAH Amma xan dinga binki da kalamai har sai nadamarki tafi haka

XARAH 'dakin Momy taje takwanta tana tuno kalaman Marwan. Wanda talura baqar magana ya gaya mata

KAMAL ko part 'dansa yayi ya kwanta yana tunanin rayuwa
Can yaji yanasan Ganin LABEEBAH saiya kira Safna awaya. cikin sauri ta'dauka Tace Yayah
Yace inasan kigano min me LABEEBAH takeyi
Tace bacci take Yaya
Yace. A ina
Tace tana 'dakinmu
Yace OK saiya kashe wayan. Ya tashi direct part 'dinsu Sagna yayi ananko yaga LABEEBAH tana bacci hankali kwance yayi Murmushi da qare mata kallo.
Ya da'de yana kallanta ahaka kafin ya koma part 'dinsa batare data sani ba

Marwan Yace mai gata kyakkyawa XARAH Saidai ta6ata wayanta
KAMAL ya kalleshi ka'dan yayi murmushi yace kar kayi wani alaye idan tsuntsun ya koma kan tane kagayamin in baka ita karka duba abinda tamin dan kasameta xakaji da'dinta.
Marwan yayi Murmushi Yace aa Wlhi Yayanah kawai dai nafa'di abinda yakef hakane. Da ace nafara ganinta kannaga Sagna ba shakka da tayi Babban nasarar sace xuciyata
Amma maganar gaskiya son da nakema Sagna yafi Wanda naji yanxu araina
Kawai kashare
KAMAL ya dafa kafa'darsa Yace kayi dai tunani duk wacce takwanta maka nayi alqawarin baka ita
Marwan yayi Murmushi Yace toh Sagna
KAMAL Yace tunani Nace kayi . Yace toh Yayanah Xanyi

.
[1:47PM, 23/10/2016] Rahamat Nalele💋: LABEEBAH ko bata tashi ba sanda ta'dauki kusan awa 'daya
XARAH ma bacci tasha abinta. Saidai bana kwanciyar hankali bane kamar na LABEEBAH

Mexai faru 😳

Bayan isha'i sunci abinci XARAH Sam takasa cin Komai duk tawani hargitse lokaci 'daya
Sagna da Safna sun tambayeta me ya hargitsa ta haka Tace ba Komai
Sumayya tajah numfashi Tace toh Allah yasa ba Komai 'din
LABEEBAH ko tunani tayi qila har yanxu tunanin wannan aljanin nata takeyi Wanda ta'dauka KAMAL ne

KAMAL yakira Momy awaya Yace plx my Momy 'dan turomin 'Yar taki man
Momy tayi Murmushi Tace naqi baxa'amin hira agida bah
Yace ayya momyna dan Allah kituromin ita magana 'daya xan gaya mata
Tace toh naji. Takashe wayan tana Murmushi

Can takira Sagna Tace mata taturo mata LABEEBAH
Nan ko LABEEBAH taxo
Momy takalleta da Murmushi Tace ga abinci nan inaso ki kai part 'din KAMAL toh Momy. LABEEBAH tafa'da da 'daukar abincin

Tunda ta doshi part din gabanta yake fa'duwa danjin qamshin turaran KAMAL
Tayi sallama tashiga falan da ajiye abincin kan table
Juyo wannan da xatayi sai taga KAMAL xaune akan kujera yana danna waya
Marwan na gefanshi yana kallanta
Taje kusa da Marwan Tace dan Allah kaima  kana ganin aljanin nan
Yace eh Sosai mah
Tace ko kaima aljaninne
Yace aa ni mutum ne kamarki Yana fa'din haka ya fitta daga falan yana mata dariya

LABEEBAH xatayi saurin bin bayansa sai taji kawai KAMAL ya rige mata hannu
Yace xauna
Ba musu taxauna a kusa dashi inda ya buqata
Ya tattara hankalinsa da nutsuwarshi waje 'daya ya kama hannayanta dukka biyu yana kallanta ido cikin ido Yace lokacin da na sauka a jirgi. Na tsaya jiran direban Kakah yaxo ya 'daukeni
Amma abin mamaki sai wani  yaxo akan wai anturo shi ya 'daukeni
Ba musu nashiga motar tasu
Ashe rayuwata suke nema my baby. Dan ban tashi tsintar kaina bah sai a wani gida wanda baxan iya cewa ga inda mukabi mukaje wannan gidanba
Sai ogansu ya harbeni harbi biyu. Sannan yasa yaransa suka jefar dani a ruwa
Daga nan sai tsintar kaina nayi a qasar Armiyaniya. Nafa'da hannun sarkin garin

Shiya bani temakwan gaggawa
Har nasami matsalar 'daukewar tunani.
Daga baya tunanina ya dawo
Sarkin ya nunamin qaunah Sosai my baby ya 'dorani akan wani business 'dinsa da yake qasar England garin Dubai
Ni ba aljani bane my baby
Ni KAMAL 'dinki ne

LABEEBAH ta kura mishi ido Tace toh me yasa da aka kawoka mugaka fuskarka akan kaine wanda ka mutu. Yace duk shirin mutanan ne ban san dalilinsu nayin hakan ba
Tace yanxu kai Ya KAMAL ne
Tashi yayi ya buqaci Tatashi
Nanko Tatashi ya ware hannunsa Yace rungumeni Ki gane
Ahankali taje ta rungumesa
Nan ta lumshe ido Tace gaskiyane kaine kai Ya KAMAL.....

Ya rabata da jikinsa da qura mata ido Yace xaki Aure ni.......
Hawaye ya xubu mata Tace ina sanka Ya KAMAL ina sanka Wlhi ina sanka ina qaunarka.
Amma ya xanyi da XARAH tana sanka. Kuma baxan iya kishi da ita bah
Ni kam na haqura da kai kawai
Ka maida matarka kawai
Yace ko
Ta'daga mai kai
Yace shi kenan
Ta qara 'daga mai kai
yaja numfashi. magana ta gaskiya Baxan maida Auran XARAH ba
Idan har ban Aure kiba Wlhi baxanyi Aure bah
Kuma nayima xuciyata alkawarin Auranki. Baxan ta6a barinki ba my baby
Yana fa'din hakan ya manna mata kiss a baki da nuna mata hanyar 'kofah
Ta kalleshi
Yace jiki dan Allah
Sai kawai ta rungumeshi tarushe mai da kuka

A duniya KAMAL bayasan kukan LABEEBAH daurewa kawai yake
Ya 'dago da fuskarta data rimtse idanta. Yace ki temaken dan Allah kidena kukannan yana ta6a xuciyata plx karkisa na aikata miki abinda baidace ba yanxu

Ta bu'de idan nata da 'dauke sautin kukan Amma hawaye bai bar xuba mata
cikin shagwa6a Tace meyasa baxan rayu cikin farin ciki bah
Yayi Murmushi Yace xakiyi rayuwa taban mamaki me da'di da gar'di da laushi da Santsi idan kikabi Komai asannu
Cikin kuka ta raba jikinta da nashi tafita daga falan.
KAMAL yayi Murmushi Yace bana san matsala tadawo min Wlhi
Ya 'daga kansa dama
Allah ka dubeni dan darajar Manzanka Annabinmu

LABEEBAH kare fuskarta tayi daga mutane tashige 'dakinsu Sagna
Anan taga XARAH duk jiki amace dan kallo 'daya xaka mata ka tabbatar a hargitse take

Aiko sai LABEEBAH bu'de shafin kuka
XARAH na kallanta

Tace meya saki kuka LABEEBAH
Shuru LABEEBAH tayi mata
XARAH tayi Murmushi Tace kinga Aljanin naki yace miki shi KAMAL ne ko
Da sauri LABEEBAH ta kalleta
Na gaya miki tun farko KAMAL ne kika musamin da aljanine
Na ganshi 'daxo ai. Hakanne ya qara tabbatar min da cewa shine
Toh mai xai dameki Bayan kinsami abinda kikeso.
Ya dawo gareki da muradin Auranki
Kibashi ha'dinkai kawai.
kuma kishare Komai aranki. Karki dubeni bare kiyi yunkurin aikata abinda ko xaki mutu baxai yuhuba

XARAH na kaiwa nan ta kece da kuka. Fa'di take na cuci Kaina LABEEBAH na aikata abinda har namutu baxai dena damuna ba
Na rasa KAMAL rasawa irinna har abada
Na aikata mishi abinda Ku xan mutu baxai qara maidani matsayin matarsa bah
Hajjiya Turai ta cuceni tasakani na aikata abinda in jama'a sukaji xasuyi Allah wadai dani
Ba xan rufe miba LABEEBAH ayan duk duniya ba abinda yake damun xuciyata kamar MASEEFAR SON KAMAL
Saidai baxan qara Kasan cewa Matarsa bah

LABEEBAH tayi shuru kawai tana jinta tana hawaye
Haka suka Kasan CE XARAH na kuka LABEEBAH na kuka

Washe gari walima
XARAH da LABEEBAH sunyi kyau Sosai cikin shigar dogajan riguna da Momy tabasu Tace shi xasusa

XARAH da LABEEBAH sunyi mamakin Cikan da akayi.
Duk wani abokin KAMAL sanda ya halacci gun
Haka kowa na Momy da Dady sanda suka bayyana kowa nuna farin Cikinsa yake na bayyanar KAMAL

Dake harabar gidan irin babbar nance. anan akayi Komai akagama
anci asha abin dai sai Wanda yagani
Haka taro ya watse cikin jin da'di
Hajjiya Kakah da Hajjiya Zainab ne sai Su LABEEBAH ne wa'yanda suka rage
Suma gobe xasu cilla garin nasu na kano
Momy ta kalli Kakah Tace ai tare dani xamu Kanon dan maganar shi KAMAL 'din da LABEEBAH.
Kakah Tace toh Allah ya kaimu
Hajjiya Zainab Tace AmEEn. Aiko gwara ayi saurin mishi wannan gatan
Momy tayi Murmushi

KAMAL ne yayo shashin Momy dan yana San kar6ar Abu agunta. Yayi kyau Sosai Cikin shigar

suit dan yanxu duk shigarsa haka take
Aiko sukaci karo da XARAH gaf
Nan ta durkusa qasa takama qafarsa takece da kuka
Tace dan Allah ka yafe min dan Allah na roqeka dan soyayyarka da Allah kamin rai nayi nadama nayi nadama nayi nadama ka rufamin asiri
Dur 'kusawa agabanta yayi shima Yace XARAH kenan.
Hmmm Kinga rayuwa ko
Haka take daman tunda ba ahannun mutum takeba
Na yafe miki har abada bawanda xaiji wannan batu.
Mutum 'daya nema wanda na gayama
shine kuma Marwan Namiki alqawarin ba nabiyunsa aji
Temako 'daya xakimin Ki birgeni shine inaso idan Momy taxo gidanku da maganar Aurena da LABEEBAH inaso kice na nemi kikoma gidana kece kikaqi
Idan antambayeki dalilin dayasa kikaqi hakan kice............

Saurin katseshi XARAH tayi cikin kuka Tace karka damu da wannan nasan abinda xance musu Ni fatana kayarda da tubana kuma kayarda ayanxu duk duniya ba Wanda nake MASEEFAR SOO sai kai ina SONKA ina QAUNARKA
Saita qara fashewa da kuka mai ban tausayi
Yayi Murmushi Yace watoh XARAH SO maseefa ne SO balaqine SO damuwa ne. SO ba da'di bane. nayarda da hakan dan nagani akan MASEEFAR SAN da nakema LABEEBAH ina santa ina QAUNARTA duk duniya ba wata macen da xatasha gabanta aguna
Yana fa'din haka ya tashi ya barta nan xaune cikin kuka

LABEEBAH taji Komai da suka tattauna dan itama 'dakin Momyn tanufa dan baxata iya jure shu'umin Kullan da KAMAL yake jifanta dashi ba
Dan haka tana ganin yabar inda suke tace bari tayo 'dakin Momy
Toh saitayi gamo da XARAH da KAMAL tanajin tafiyarshi yanda yanajin kukan XARAH yayi burus da ita shiyasata sulalewa ta xube aqasa tana hawaye. To wai wane lefi XARAH tayi mishi hakane

Ita dai tana San XARAH tanasan farin cikinta gashi farin cikin nata ya bayyana agareta Saidai yaqi yarda ta ra6eshi Sam

Gashi ita kuma abinda takeso shine farin cikinsu dukka ita da XARAN
tanasan KAMAL Amma baxata iya Auransa XARAH tana gani bah
Ta kece da kuka ta'dora hannu aka Tace wai har sai yaushe xan dena shiga matsala asoyayya har sai yaushe
Haba soyayya meyasa baxa kimin adalci bah
Meyasa kike tarwatsa nutsuwata
Meyasa in nan ya toshe saiki 6ullomin tawani gun
Wai KAMAL ne ka'dai namiji aduniya. Daxaki nace mishi xuciyata.
Haba haba haba xuciyata meyasa kikesan KAMAL
Sam banyi dace da soyayyaba

Na tsina kaina na tsani kaina taqara rushewa da kuka

XARAH najinta tatashi taxo lungun da take takama hannunta Cikin xubar da hawaye  Tace KAMAL nakine LABEEBAH tun farko
Tabbas nayarda da qaunar da kikemin Amma kisani idan MASEEFAR SON KAMAL xata kasheni baxan kumama Auransa ba har abada
Nabar miki KAMAL

LABEEBAH Tace banyi mah kaina adalci ba XARAH natsani Kaina KAMAL shika'dai namiji da xuciyata xata nace sai shi
Na rasa wanda xanso sai mijinki
XARAH tafara goge mata hawaye duk da nata ba dena xuba mata yayi ba.
Tace kimanta abinda namiki akan YUSUF ne
Kin manta irin budurcin dana miki akansa
Kin manta cewa banji tausayinki ba akansa
Toh mexaisa kidamu dan KAMAL ya bayyana agareki
Yana sanki LABEEBAH tun ranar Farko
Ki temaken ki rama abinda namiki mana akan YUSUF
LABEEBAH Tace kishare wannan XARAH yarigada ya wucce. Ki fahimceni yanxu .

ina ina ina  baxan iya Auran KAMAL kina kallo bah
XARAH Tace hmm ni kuma nayi miki alqawarin sai kin Aure KAMAL ina kallo dan KAMAL baxai ta6a barinki bah

In gaya miki wani sirri Wanda idan kaka jure a Auran KAMAL xaisa ya qara sanki
LABEEBAH ta girgixa mata kai Tace aa Karki gayamin komai
dan ke xaki koma 'dakinki mijinki
XARAH ta miqe Tace ko kiso ko karkiso LABEEBAH sai kin xama MATAR KAMAL......

XARAH tayi tafiyarta
LABEEBAH tabita da kallo
Wannan ranah kowa yasan XARAH da LABEEBAH basa cikin nutsuwarsu
KAMAL yakira LABEEBAH awaya
 taqi amsa kiransa
Murmushi yayi dan yasan abinda takeso dai bamai yuhuwa bane

Washe gari haka Su LABEEBAH da Momy kakah Hajjiya Zainab Safna Sagna Su salima 'ya'yan Hajjiya Zainab suka garyatu garin na kano
Sun sauka lafiya
Inda direba ya kai su LABEEBAH Gidansu

Su innah sunyi da murnar dawowarsu ba kamar SAUBAN daya maqale maman nasa LABEEBAH
Bayan sun huta LABEEBAH tafa'da tunanin yanda suka wanye da KAMAL harya rikita mata kwanya

Abin da ya faru ko shine
Bayan sun tashi da safe KAMAL yaje ya marairai cema Momy Yace plx momy xanyi ganawar qarshe da 'yarki kafin sutafi
Tayi Murmushi Tace hmm dakayi hakuri tare damu ni da Dadynka xamu Kanon dan maganar Auran naka da ita
Da sauri ya kama hannun Momyn cikin murna Yace naji da'di momy dan kin rufamin asiri dan Wlhi 'Yar taki ta har gitsamin tunanina
Tace yanxu dai ina bakayi breakfast ba Yace eh Tace kaje xan turo maka ita. Yace Yauwa momyna

Yana fitta ko Momy takira LABEEBAH Tace takaima KAMAL breakfast 'dinshi
LABEEBAH dai toh tace mata Amma xahiri bata so ba

Da sallama tashiga falan nashi ta ajiye Komai kan table.
Marwan ya kalleta Yace gdmning my Aunty da fatan kintashi lafiya
Tace lafiya lau. Sannan Ta kalli KAMAL ka'dan Tace ina kwana Ya KAMAL
Yace daban kwanaba zakiganni
Tace atunanina banyi lefiba.........
Marwan ne ya fitta dan basu guri
KAMAL ya kalleta da kyau. Sai tayi saurin sunkuyar da kanta
Tace akwai abinda kake buqatane dan.....

Katseta yayi wajan tashi ya nufeta.
Yace jiya lefin menayi kikaqi 'daukar wayata
lumshe ido tayi dan jin qamshin sweet 'din bakinsa Tace wayan fah bata gurinane
Yace tana gurin waye
Tace Sumayya.
Yace yaushe kika fara qarya
Taqara lumshe ido dan qamshin sweet 'din yana neman takura mata dan jinshi take kamar ita takesha
Yayi Murmushi Yace xaki Sha ne
Tabu'de idanta ahankali bata san lokacin data 'daga mai kai bah
Ya qarayin Murmushi xaiyi magana XARAH tashogo falan duk suka bita da kallo
Ta koyi saurin runtse idanta dan baqaramin mummunan gani tayi ba
Dan xuwa lokacin da tashigo falan hannayan KAMAL Suna kan qugun LABEEBAH yayinda fuskarsu ka'dan ta rage ta ha'de da juna dan kusanci
Cikin saurin XARAH tamaida kanta qasa takasa cewa Komai danta manta abinda ya kawota mah tayi
KAMAL ya maida Kallansa ga LABEEBAH cikin 'daure fuska yayi furucin nashi ahankali yace

bu'de bakinki tayi narai narai da ido tanasan xubo da hawaye. Yaqara 'daure fuska
Aiba shiri LABEEBAH tabu'de bakinta yasaka mata sauran sweet 'din da yake bakinsa tare da manna mata wani shu'umin kiss a wiya. Nan tasaki wata qaramar qara
wani Abu ya caki xuciyar XARAH hawaye ya xubo mata nan taficce da gudu batare da tayi abinda ya kawota ba.

Hawaye ya xubuma LABEEBAH cikin kuka Tace Ya KAMAL........
Yayi katseta da cewa ke kike da damar mallakarsa
Tayi shuru
Yaci gaba da fa'din
Wlhi daga yau kika qara min xancan XARAH ko ina tare dake kika ganta kika wani Sha jinin jikinki kin san Allah ba abinda xai hanani hukuntaki
Cikin shagwa6a tace to ya Xanyi. Yace wannan kuma ke kika sani
Tace ai matarkace koka manta kata6a Auranta harda arxiqin 'da.......
Cikin jin haushinta da maseefa ya raba kansa daga gareta ya nunata da yatsa Yace Wlhi daga yanxu kika qaramin manarta saina miki dukan tsiya
Tace toh meyasa baxa duba halin son ka da yake damunta kayi mata afuwa sai ka maida ita gidan.......
Wani wawan mari ya sakar mata wanda tunda take ba'a ta6a yimata irinshi bah
Dan haka cikin sauri ta durkushe agabansa tarushe da kuka

KAMAL ya yabi hannunsa da kallo tare dajan wani shegen tsaki. Yakama kansa cikin takaicin abinda ya aikata Yace am sorry
Tashi LABEEBAH tayi daniyar fitta daga falan yace kitemaken ki yafemin my baby.
Tayi banxa dashi. Ganin haka yasashi saurin jawota jikinsa cikin sanyin yanayi yana shafa bayanta cikin lallashi Yace am sorry
Cikin sanyin itama LABEEBAH Tace dan Nace kamaida.......
kanta qarasa yayi saurin katseta da cewa idan kika qarasa saina sharara miki marin dayafi wannan yanxu wlhi
Shuru tayi kana taraba kanta dashi sannan ta fitta daga falan
Ya bita da kallan Takaici da harara

XARAH ko dama Hajjiya Zainab CE tasata kiran LABEEBAH dan shirinta ne yarage musu
Qaddara tasata amsawa dabin umarninta
Tafitoh falo ne Sagna Tace naga tayi shashin Ya KAMAL 'daxo
gaban XARAH yafa'di har xatace Sagnan ta kirata sai kuma tafasa
Ashe da raban xatayi mummunan gani
Tafashe da kuka tanajin wani MASEEFAR SON mijin nata ga qaddarar mummunan halinta tayi mata yankan qauna.
Cikin kukan Tace Turai kin cuceni......
Sumayya dake kallanta Tace hmm Allah ya kyauta
XARAH ta galla mata harara da ficce daga 'dakin

Koda LABEEBAH taje 'dakinsu Sagna bataga XARAN ba
Nan takafa tagumin me xatace mata
Aiko tana cikin tunaninne XARAH tashigo 'dakin
Sai dai LABEEBAH ta tsinci kanta da basarwa tayi kamar basuyi Komai da KAMAL 'din a gabanta bah......

SAUBAN ne ya katse mata tunaninta da cewa menene momyna me yake damunki kikayi shuru
Tashafah kansa tare da kai masa kiss agoshi Tace Dadynka ne yake damuna SAUBAN
Yace toh meya miki. Waro ido tayi danjin ashe a bayyane tayi furucin
tayi Murmushi Tace kanajin bacci Yace eh
Tace toh xumu kwanta haka ko suka kwanta abinsu
Sai dai kuma Suna kwantawae taji sa'ko ya shiga wayarta
Nan ta 'daubah da dubawa
_momy xata baki maganinki dan a lissafina yau saura kwana uku al'adarki taxo miki plx kitemaken kifara Sha goben pls my baby_
[10:13PM, 27/10/2016] Rahamat Nalele💋: Tayi Murmushi tace abayyane Ya KAMAL
Cikin sauri tarubuta mai
_Baxan shaba_😔
Sakwan na isa ga KAMAL yayi Murmushi ya mayar mata da _ai baki isa ba. Kina sone Ki hargitsani inrasa tunanina da nutsuwata_
_tace hmm fuskata fah ta kunbura_
KAMAL ya waro ido. Cikin sauri ya kirata
Ashagwa6e tace hello
Yace am sorry my baby pls Ki kiyaye gaba banasan kiramin xancan XARAH plx
Tace to Amma......
Ya katseta da fa'din Ya salam
Cikin sauri Tace toh kayi hakuri nadena
Yace gud kin temaki kanki. Yanxu dai bani labari kina inane me kikeyi me yake faruwa
Taturo baki tamkar tana gabansa Tace ina kwance nida SAUBAN muna San muyi bacci
Yace da kyau babyna kuhuta lafiya. Am gobe xani qasar Armiyaniya ina buqatar addu'ar Ki
Tace Allah ya kaiku lafiya ya dawo daku lpy Yace AmEEn AmEEn
Tace Ya KAMAL......
Yace ke kike da damar mallakarsa
Tayi Murmushi Tace dama inasan sanin duk xamanka a qasar baka ta6ayin budurwa bah
Yace hmmm fa'da miki ne banyi bah. inada mata acan.
Tayi saurin tashi cikin wani yanayi Tace yanxu kana da mata kuma kakesan mallakata.
Yayi Murmushi Yace karfa Ki damu my baby tana sanki ba 'dan ka'danba
Dan Kullun xan canta gareni yaushe xata ganki. Fa'di take ina San Aunty Laveevah dan Allah kakaini gunta
Nakan ce mata xan kawota gunki.........
Cikin wani yanayi LABEEBAH ta katseshi da cewa Wlhi qarya take dan ba matar da takesan budurwar mijinta.
KAMAL ya gyara xama Yace aa fah😳 da gaske khadi take tana sanki

Cikin maseefa tace toni bana  santa kuma baxan sota ba danna tsaneta...... Tana fa'din haka takashe wayan gabaki 'daya
KAMAL yayi Murmushi axuci yake fa'din bawacce xata qara gigin mallakata saike my baby ina matuqar sanki

LABEEBAH kuka tafashe dashi tsakaninta da Allah tanayi SAUBAN na tayata dan ganin kukan da take ba nawasa bane

Daqir KAMAL yasamu kanta da daddare Bayan ya qaryata kansa dace mata wasa yake mata

Washe gari XARAH na xaune agidansu takalli Innah da baba da suke karin kumallo
Tace BABA
Yace na'am
Tace dama KAMAL ne yakesan LABEEBAH
Babah da Innah fuskarsu tacika da fara'a atare sukace kai Amma ko munji da'di Kinga sai ya ha'daku tunda bakwa tare da matsala
XARAH tagirgixa kai
Tace xan cutar da LABEEBAH tabbas inna qara kasan cewa da KAMAL kamar yanda nacutar da ita a gidan YUSUF
Kuma kafin KAMAL ya 6ata na aikata mishi wani lefin da baxan iya komawa gidansa ba
Koda ko ya buqaci hakan
Innah tayi sak hakama BABAH
Candai BABA Yace toh keko XARAH wane lefi kika aikata mishi haka
Hawaye ya xubu mata tace Wlhi Babban lefine mummuna
Kuma baxan iya gaya muku ba. Dan sirrine tsakanina dashi
Ni dai ina roqarku da Allah karku saka wani abu aranku dan gane da Auransa da LABEEBAH
Cutace dai na cuci Kaina
Dan Allah ya ha'dani da hatsabibiyar qawa wacce takasa bani shawara tagari
KAMAL yayi min halacci tunda ya iya 6oye abinda namasa. Hakan yasa nima baxan iya furtama kowa ba.
Innah Tace tomu kigaya mana mana.........
Babah ya katseta da cewa aa Karki matsa mata. qila abin ba  alkairi bane. kuma da tanaso muji data fa'da mana tun farko
Innah tagya'da kai Tace hakane toh Allah ya kyauta
Dama Momyn taku Tace yau xataxo da yamma ita dasu Dady qila maganar LABEEBAN CE.
jiya takirani take gayamin
Babah Yace toh Allah ya kawosu Kinga na dawo da qarfe uku dan susa meni
Innah Tace ya dace kam

Yamma nayi ko Su  Momy sukaxo da maganar Auran KAMAL da LABEEBAH

Toh Madallah Komai yaxo da Sauqi dan anbada sadaki da Komai
Har akayanke biki wata 'daya me xuwa

LABEEBAH tabasan Komai akan lamarin bah
Sanda Su Momy suka tafi Sumayya takawo mata tsegumin.
Aiko LABEEBAH ta xabga tagumi da fa'dawa tunani
Ga dai KAMAL tana shirin mallakarsa Amma damuwa da fargaba sun cika xuciyarta
Sumayya Tace yanaga kin shiga tunani
Rukayya tayi Murmushi Tace ai dama nasan qarshen wannan game 'din naku haka xai kasance tunaninki bangane shine KAMAL 'din nakiba
Shuru LABEEBAH tayi musu tajawo maganin da Momy tabata 'daxo nan ta6alla tasha dan tafara jin marar tata tafara mata ciwo

Armiyaniya
KAMAL Suna qasar Armiyaniya inda ya gwarfana gaban Sarki ya gaya masa ainiyin Waye shi da dalilin da yasa har sarkin ya sameshi
Cikin ladabi Yace kayi BABANA ha'ki'ka bamma Kaina adalci bah tunda na iya in fa'da maka gaskiya kayimin afuwa dan Allah kaya femin
Sarki yayi Murmushi Yace koma dai menene nayafema tunda kayi hakanne da wata manufarka Amma inajin tsoran rabuwa dakai
KAMAL Yayi Murmushi Yace aini nakane BABANA
Sarki ya qarayin murmushi yace matsalar 'dayace shine iyayanka baxasu yarda Su bar min kai bah
KAMAL yayi shuru dan gaskiyane yasan Su Momy kam baxasu yarda subar ma Sarki shiba

Sati 'daya KAMAL yana Armiyaniya
yau ne shida Marwan suke shiri akan gobe suyi dubai
KAMAL ya 'dauki wayarshi da take ringing cikin saurin Yace Dadyna
Dady Yace kaxo fa'dar Sarki babanka ka samemu
Da mamaki KAMAL ya kalli wayarsa nan ya tabbatar da Dady yake waya
Sai Yace toh da kallan Marwan Yace kaji wai Dady yaxo wai yanxu haka Suna fada
Marwan ya ficce da gudu yana cewa saina rigaka ganinsu
KAMAL yayi Murmushi ya bishi

Aiko nan yaga Dadyn shi da Dadyn Salim da Sagna da Safna da Salim
Yayi mutuqar murna da ganin Su
Momy Tace kayi mamaki ko
Yace Sosai ma dan bayaune nayi tsammanin xuwanku bah
Tace Dadyne ya shirya maka wannan baxatan anayin maganar Auranka da LABEEBAH Yace toh mushirya xuwa

Yace naji da'din hakan Dady

Kwana biyu Su momy sukayi Suna ma Sarki godiyar yanda yariqe musu KAMAL
Sannan sunga karamci agun mutanan gidan
KHADIJA ko tana nane da momy ita da Halima suna jin Santa aransu dan Momy mutumce
Sarki da Dady sun tsaida xance akan KAMAL xai tsaya mah Sarki akan kasuwancinsa na Dubai
Sannan shi KAMAL Yace xaibu'de asibiti nakansa anan Abuja manyan doctors Su kafa asibitin xai dinga xuwa lokaci xuwa lokaci
Dady yaba Sarki hakuri akan KAMAL dai xai dinga rayuwarsa agarin na Abuja
Yadai xamadai KAMAL xai tsayama Sarki akan kasuwancin Sa
Maganar xaman rayuwa dai yana tare da iyayansa
Sarki yayi murna mah da hakan dan bayaso KAMAL ya ku6uce masa gabaki 'daya
Ahaka Su Momy suka dawo xuciyarsu cike da qaunar Sarki da iyalansa

Lamarin XARAH dai sai ido taxubama KAMAL da LABEEBAH dan soyayya tsalaninsu sai sambarka
Dan LABEEBAH idan KAMAL ya kirata manta kanta take haka xata xage susha soyayyarsu ita da shi gwanin tafiyar tata
[10:59PM, 27/10/2016] Rahamat Nalele💋: XARAH takan kulle kanta a'dakinsu ko bayi tayi kuka tayi kuka San ranta
Sam jitake tatsani kanta meya kaita aikama KAMAL haka tasani da yanxu tana tare da mijinta

Ana saura sati biyu biki Momy takira XARAH da LABEEBAH akan tanasan Su xauna kusa da ita na wani lokaci kafin xuwan bikin
Nan ko gyara LABEEBAH take sanyi kawai
Aiko LABEEBAH ta gyaru agun Momy
Dan maganin mata ingantattu Momy tadinga 'dirka mata
Har saida LABEEBAH takai tana canja pain sau biyar a rabah
Abin dai sai Sam barka Amarya LABEEBAH tasha gyara na bam mamaki
Sai ana saura kwana uku biki Su LABEEBAH suka dawo kano dasu Sagna
Kuma aranar Su Kakah suka kawo kayan Auran LABEEBAH
Hmmm mekaratu kaxo gidana ni Rahamat kasha kallo😂

Sagna da Safna ne suka saka LABEEBAH agaba suna yimata make-up dan yaune walimar bikin nata
Tayi kyau Sosai cikin shigar wani shegen les me colour na sky blu
XARAH ma haka
Dan anko sukayi
Walima ka'dai LABEEBAH Tace tanaso acewarta albarkan Auran suke nema

Anyi walima me ratsa xuciyar me imani
Inda malamai mata sukayi wa'axi me burkita xuciyar mutum yaji yanasan bautar Allah da San manxansa
Anci ansha an Washe

Washe gari ya kama jumma'a haka aka'daura Auran *KAMAL da LABEEBAH*

Gaban LABEEBAH ya yanke ya fa'da
XARAH tafashe da kuka
Dama ya kasance daga XARAN sai LABEEBAH da qawayensu Su biyu a 'dakin
XARAH Tace nacuci kaina
LABEEBAH ta kalleta ka'dan hawaye ya xubo mata Tace Ashe xan xama *MATAR KAMAL.......*
Wayarta tayi ringing tana kallan KAMAL ne ta 'dauka dayin shuru
Yace Allah ya cika min burina yau na mallakeki matsayin matata
Dama na gaya miki insha Allah xamuyi rayuwa me da'di me gar'di me sanyi me santsi
Inaso kice ina sanka KAMAL ina MASEEFAR SONKA. Hakan xaiyi min da'di my baby.

Cikin kuka wiwi Tace wannan kalmar itace kalmar da harshena ya kware wayan fa'darta
Ina sanka KAMAL ina MASEEFAR SONKA
Gaban XARAH yayanke ya fa'di. Tabbas LABEEBAH tagama samun KAMAL
KAMAL ya gama samunta tunda gata kusa da ita Amma tafurta Kalmar tanasan KAMAL kuma agabanta
KAMAL yajah numfashi Yace ke ka'daice macan Aurena har abada. Kisani ko a aljanna ina ina addu'ar Allah ya barni dake
Ina MASEEFAR SONKI

Ki shirya xama dani
Dan na tanadar miki wasu abubuwa wanda na'dau shekaru ina tara mikisu

Idan kin tsallake kwanciya a qirji na yau.
Gobe bazaki tsallake ba..........
Nayi miki wannan alqawarin
LABEEBAH taqara saka kuka
yayi saurin kashe wayan nasa
XARAH taxuma LABEEBAH ido
LABEEBAN ta kalleta ido cikin ido Tace ina matuqar ~*MASEEFAR SON KAMAL*~

XARAH ta goge hawayanta Tace nasani
Tana fa'din haka tabar 'dakin
'Daya daga cikin qawayan nasu Tace da LABEEBAH nidai wannan Abu yaban mamaki XARAH ta Aureshi a karan farko gashi ke kin aureshi a karo na biyu
Shuru LABEEBAH tayi mata

Cikin wannan ranah LABEEBAH tasha nasiya daga Su innah da Ya Usman har Rukayya
Tayi kuka San ranta
Haka tanaji tana gani aka kwashesu xuwa Abuja. Shikenan tabar gida har abada kuma ba'a mata fatan tadawo taqara rayuwa irin tada agidan

Dare baiyi can bah suka iso Abujah tunanin LABEEBAH gidan da akakai XARAH nan xa'a kaita ashe ina ba nan bane
Wani shegen gidanane akakaita inda ya hargitsa kowa.
Gidane Wanda ya amsa sunansa gida
Gida ne Wanda duk mesan duniya xaiso dama shine ya mallake shi

Rayuwa kenan me xuwa da canji kala kala
Rukayya da Sumayya XARAH sun taya LABEEBAH kwannan gidanta
Amma kallo 'daya xakama XARAH kagane tana Cikin wani hali da takura
Dan ita da tayi niyar qin biyosu Sam
Amma daga baya tacanja ra'ayi

Washe gari Komai yatafi yanda akeso
Dan haka Su XARAH suka cale garin na KANO
Duk da Momy bataji da'din hakan bah. Amma sun bata uxiri

Bayan tafiyarsu momy takira LABEEBAH awaya tana bata hakuri ta kwantar da hankalinta dan Sumayya da Rukayya sun gaya mata irin kukan da LABEEBAn takeyi
Tace toh Momy

Su Sagna da Safna da Khadija da Halima yaran Sarkin Armiyaniya ne kawai suka rage agidan LABEEBAH sai SAUBAN 'dinta
Khadija da Halima sun qarema LABEEBAH kallo tsaf sun gano tafi kyau afilima
Gaskiyane KAMAL yayi dace da mace
Itama LABEEBAH tana binsu da kallo dan bata sansu adangin Su Sagna ba
Can dai takasa hakuri ta tambayi Safna suwaye
Tace yaran Sarkin daya riqe Ya KAMAL ne
Tace ayya shiyasa ban sansu bah

Can dare suma suka watse mata. Ta kasance ita 'daya kwal dan har SAUBAN sanda sukamai

wayo bata saniba sukayi gaba dashi dan Momy ta garga'desu akan karsu barshi
Sai da suka tafi ta'ankare. Aiko taji haushin hakan

Bayan tayi sallar isha'i ne tayi kwanka da saka wata atamfah me launin pink tayi kyau Sosai aciki riga da siket ne
Kayan sun matseta yayin da Komai ya bayyana agareta
Tafeshe jikinta da turare tabi gado tana tunanin rayuwa

Saidai batayi nisa a tunanin nata ba taji shigowar Su KAMAL kusan su biyar ne
KAMAL ya shigo 'dakin ganinta kwance yasashi yin Murmushi tare da xama kusa da ita
Ya 'dagota jikinsa da rungumarta
Itama ta langwa6emai
Cikin wata murya Yace Babyna
Tace na'am
Yaja numfashi da shaqar qamshin kanta
Yau gaki ga Ya KAMAL 'dinki
Tace nayi farin ciki da wannan ranah
Yace nafiki farin ciki fah
Tayi Murmushi da qara shige mai
Cikin wani yanayi ya 'dago ha6arta yana qarema fuskar tata kallo
Ta lumshe ido
Sai yakai bakinsa kan idanta ya kissing
Ta qanqa meshi dan jin wani xirrr da taji

Ya gyara mata xama Sosai akan ciyarsa. Sannan ya kira Marwan awaya Yace Su shigo kawai
Aiko kan LABEEBAH ta ankare saijin shigo warsu kawai tayi
Allah yasa da gyale ajikinta. Ta6oye fuskarta a girjinsa
Abo kana Yan nasa sukayi sha'awarsu ahaka
Yayinda LABEEBAH takasa motsi ko ka'dan tayi lub ajikin KAMAL tana jinjina tantirancin KAMAL
Haka suka gama saka musu albarka a cikin Auran nasu
Tare dayima LABEEBAH nasiya Sosai
Sannan suka ajiye musu kaxa da madara suka ficce
Suna fita LABEEBAH ta zare jikinta daga na KAMAL tana turo mai baki
Ya lakuce mata hanci Yace kiyi alwala kafin nadawo daga rakasu
Tace ai ina da alwalata
Yace Yauwa da ficcewa

Ko cikakken motsi batayi ba taji har yadawo yana kulle gidan
Can sai gashi da cup a hannunsa yasa agefe
Tare da shinfi'da musu dadduma Yace tashi muyi sallar godiya ga Allah daya ha'damu matsayin ma Aurata
Ba musu Tatashi yajasu. Bayan sun idar ne ya dafa kanta yayi mata addu'a yayi mata tambayoyi akan yanda take wankan tsarki. Tabashi amsa

Daga nan ya fuskanceta da kyau Yace kisaka kayan bacci
Tace toh kafuta innasa saika dawo
Yayi Murmushi Yace basai na fittaba my baby Kinga na rufe idona mah
Taje ta bayansa ta kulle masa ido da 'dan kwalinta Sannan ta'dauki wasu riga da wando masu santsi kuma shara-shara- suke
Tayi toilet tasaka Sannan tadawo ta kunce masa furskar tasa
Yayi saurin janyota jikinsa suka saka dariya lokaci 'daya
Yace watoh keme wayo ko
Tamai fari da ido
Ya manna mata kiss da lakuce mata hanci.

Zaki sani ne ai. Yafa'da da saka mata kaxa agabanta da madara

Sai tayi saurin gir gixamai kai alamar takoshi
Yayi murmushi Yace meyasa my baby
Tace hmm nidai na qoshine kawai
Sai ya fara lallashinta cikin sanyin murya Yace haba Babyna najifah tun safe bakici Komai sai aikin kuka
Tayi shuru
Ya qara maqaleta a jikinsa ya fara bata naman tana ci da madarar
Da'di ya cikashi yana bin bakinta da kallo tamkar ya cinye mata shi dan maseefar sha'awar kiss 'din daya bijiro masa
Sanda ta qoshi tam ya barta Sannan yafacin sauran
LABEEBAH tajita jikin masoyinta abinda take yawaita mafarki akai dan haka kan yagama cin sauran kaxar tayi mai bacci
Ya bita da kallan Murmushi ya shafi fuskarta ka'dan da manna nata kiss
Sanda baccin nata yayi nisa Sannan ya 'dauke ya kaita bet room 'dinshi ya kwantar da ita kan ni'iman taccan gadansa

Sannan yayi toilet yayi wanka ya saka kayan bacci da turare yaxo ya rungumi abarsa
Saidai yakasa jurar kasan cewa da ita ahakan
Dan haka ya fara mata tafiyar tsutsa ta cikin gashin kanta
Cikin mayan bacci Tace Ya KAMAL.......
KAMAL yayi shuru yana tunanin duk duniya ba wacce yake jin da'din sunanshi abakinta kamar LABEEBAH
Yace Mene ne
Tace inajin wani iri
Yace haka yadace jiki
Aiko saiji tayi ya rabata da rigarta
Gabanta yayanke ya fa'di tabu'de idanta nan jikinta yasoma rawa dan ganin ya xubama dukiyar fulaninta ido yana ta6asu yana wasa dasu
Tajah numfashi
Cikin kwarewa yafara tsotsarsu yana sauke ajiyar xuciya
LABEEBAH ta lumshe  idanta hawaye ya xubo mata

Nan KAMAL ya 'dau lokaci yana abu 'daya yayinda hankalin LABEEBAH yatashi dan ganin kamar bashi da niyar bar mata Su a qirjinta. Gashi sun fara yima xafi da ra'da'di
Saita fashe da kuka anan KAMAL ya'dan saurara mata sai kuma ya fara Uwa da ubah
Saijin ihun LABEEBAH kake da wani axababban kuka. Amma Sam KAMAL bai saurara mata ba
Ahaka tasume mai duk da ya ankare da hakan Amma yacigaba da hidimar gabansa
Yi yake yana kuka wiwi dan LABEEBAH taxo mishi da bama bamai Wanda ya zautar dashi daqer yasami kansa
Duk da yasan tasume hakan baisa xuciyar shi hakura bah dan qara kwadai tuwa yayi da ita
dan haka yaqara sauke abubuwan nashi da yace ya 'dauki shekaru yana tanadar mata Su

Sanda ya tsaftace kansa yasami sarki Sannan yaxo yayi lafula raka'a hu'du yana godema Allah daya mallaka masa LABEEBAH matsayin matarsa

Kana yaje ya shafa fuskar LABEEBAH Yace am sorry my baby kinshigo sabowar rayuwa
Sannan yabi xanin gadan da kallo Kasan cewarshi fari yasa shi ganin 6arnar da yayi
Yayi Murmushi da kin kimarta sai toilet

Ba qaramin qara LABEEBAH tasake ba wajan jinta da tayi cikin ruwan xafi
[1:15PM, 28/10/2016] Rahamat Nalele💋: Cikin kuka Tace Ya KAMAL karka kasheni dan Allah
Yace idan na kasheki inyi rayuwa dawa
Taqara fashewa da kuka
Baiyi gigin lallashinta ba dan yasan ba sauraransa xatayi ba
Haka ya gasata tana mishi ihu yana rufe mata baki
Sanda ya tabbatar da tagasu Sannan yakai bakinsa kunnanta Yace in miki wankan sarkine ne
Ta gallamai harara tare da cigaba da kukanta
Yace idan bakimin magana bah Wlhi xan qarayi
Tayi saurin kallansa Tace ashe baka da tausayi Ya KAMAL
Yace eh tadai wannan bani dashi
Tace toh jeka xanyi kayana Yace aa fah in baxaki iyaba in miki
Me makwan tabashi amsa saita qara fashewa da kuka dan ba'abinda take buqata ayanxu kamar yabar ta
Yayi Murmushi ya ficce daga toilet 'din
Tabishi da kallan harara

Canxa xanin gadan yayi yasaka wani Sannan ya feshe 'dakin da turare
LABEEBAH dai data gama komai tatashi da niyar tafiya sai taji takasa
Idan kuma tamatsa saidai tatafi a tale ga xafi
Dan haka sai kawai taxauna taci gaba da kukanta
KAMAL ya leqa toilet 'din Yace baby yadai
Cikin kallan harara Tace ni nakasa tafiya
Ya waro ido kamar gaske Yace Subhanallahi abun yakai haka
Tayi saurin 'damai kai cikin shagwa6a
Shiga yayi Murmushi akan fuskarsa ya 'dauketa
Sanda suka fitoh ya qura mata ido Yace kina da abubuwa masu da'di babyna.

Taturo baki tace ni kakwantar dani
Ya kwantar da ita da saka mata wata dogowar riga sai shima ya kwanta ha'de da rungumarta.
Yace naqara sanki ina qaunarki plx kar kiyimin rowar kanki pls.
LABEEBAH najinshi yanata mata sambasu tayi shuru bacci yayi awan gaba da ita
Bai ankare da hakan ba sanda yaji numfashinta Sannan ya gane bacci ya 'dauketa
Yayi Murmushi Yace sabowar rayuwa

Da Asuba Bayan yatashi yayi alwala da tsaftace bakinsa
Yaxo dai-dai kunnanta Yace allahu akubar
Har cikin ranta LABEEBAH taji Amma bata tashiba
Yafita xuwa masallacin unguwar yana jin kansa kamar ya sauke wani kaya me nauyi wanda ya takura mishi da

LABEEBAH najin fitarsa tayi qarfin halin tashi tayi toilet jiri na ibanta ga wani maseefar xaxxa6i daya caf keta
Duk jikinta ciwo yake mata. Bata ta6ajin ciwo irin na yau ba
Haka tacanja kaya tayi Sallah. Ko addu'a batayi ba takwanta akan daddumar kanta na sarawa
Awannan yanayin KAMAL yadawo ya sameta
Hankalinsa ya bala'in tashi haka yabata madara da magani
Cikin lokaci qanqani tayi bacci
KAMAL ya xuba mata ido
Dama yasan LABEEBAH ba iya 'daukar abubuwan nan nasa xatayi bah
Yaja numfashi Yace ina sanki matata

Da gari yayi haske momy ta aiko musu da breakfast
Sai kusan Sha 'daya LABEEBAH tatashi
Ba lefi tasamu qarfin jikinta Amma ciwo ba abinda ya ragu
Tana kuka KAMAL yayi mata wanka yasaka mata Kaya da fesheta da turare yana cewa anfisan mace takasance da qamshi ako wane yanayi take
LABEEBAH tajah numfashi da kwantar da kanta a qirjinsa
Yace pls kar kiyimin kuka fah
ta kallesa da shanyanyun idanta Tace dama haka Aure yake Ya KAMAL
Yace eh... Sosai ma
Tace Amma nidai idan kaqarayi mutuwa xanyi Wlhi
Ya kama fuskarta ya fara aika mata da wani lafiyayyan kiss
Yace baxaki mutuba babyna
Dan yauma xan qarayi dan kisaba dashi
Ta waro ido da 6ata fuska xata fashe da kuka
Yace yi hakuri wasa nake miki
Kuma Wlhi kidena min kuka akan Komai dan inna saba da kukanki Gaskiya akwai matsala
Ta qanqameshi tana cewa idan dai xaka kara xanyi kuka harda koke koke
Ya 'dauketa sukayi dining ya direta kan cinyarsa Yace hmm baxama qaraba bare kiyimin asarar

hawayanki
Tayi murmushi.... Lokaci 'daya kuma kanta ya Sara ta dafe kan
Yace kodai ciki ya shiga ne a daran na jiya shuru tamasa dan jin kan ya'dan saketa
Ta bu'de baki ya dinga bata abincin tana xubamai shagwa6a

Satinsu 'daya yana jinyarta kuma bai qara kusantar taba
Kaf KAMAL yagane Sosai LABEEBAH xatayi ragwanta
Toh Ya xaiyi da ita ko nace ya xaiyi da kansa danshi dai mabuqacine bana wasa bah
Abinda yasa yaqara San XARAH kenan a xaman Auran shi da ita dan Gaskiya ita'din jarumace dawajan wannan har kar

Tausayin kansa ya kamashi dan yasan kafin LABEEBAH ta saba da lamarin xai bata wahala Ya dafe Kansa
LABEEBAH ta kama fuskarsa tayi mai kiss Tace me Nene Yayana me yake damunka tunanin me kakeyi
Ya kalleta da Murmushi Yace ke kike damuna baby ako yaushe tunaninki shine abu nafarko daya ke damuna
Tace toh gaya min yanxu me nayi
Ya kai hannunsa kan breast 'dinta Yace ina sansu baby daxaran na buqacesu xaki hauyimin kuka Sannan ba abinda nake buqata atayuwa ayanxu kamarki. Ya Xanyi baby....
Yafa'da da dafe kansa
Jikinta yayi sanyi hankalinta kuma yatashi dan ita atunaninta ya hakura da lamarin kenan Ashe lanfo yayi mata
Hawaye ya xubu mata dan har yanxu ciwo ba barinta yayi ba
Yanxu taji xaxxa6i anjima taji ciwan kai.
Kai ita ko ina na jikinta damunta yakeyi
Tace toh idan kaqarayi shikenan
Ya girgixa mata kai alamar aa
Saita fashe da kuka
Haushinta ya kamasa Amma yaxaiyi haka ya lallasheta dace mata idan ya qarayi shikenan

Haka ya qara burkitata awannan dare danma taji dama dama ba kamar na farko ba
Gaskiya ne tatabbatar baqaramin wahala xatasha agun KAMAL bah
Haka ciwo ya dawo mata sabo fill yayi jinyarta da damuwa
Dan duk iya bincikensa yagano ba wani abune yake damunta ba face rashin sabo da kuma ragwanta

LABEEBAH Suna waya da XARAH da kowa na gidan nasu Kullun
Saidai LABEEBAH ta lura kamar dolece takesa XARAH amsa wayanta nata

Momy ta turoma da LABEEBAH kayan gyaran jiki kuma har kiranta tayi Tace tayi mata alqawarin xata dinga Sha
LABEEBAH tayi mata alqawarin
Hakan yasa kusan Kullun LABEEBAH tana maqale da sinadaran dan akwaita dasan xaqi.

KAMAL lalla6a LABEEBAH yake kamar kwai Sam bayasan damuwarta matsalarsu dai akan sunna ne

Yau watansu 'daya Amma kwata kwata sau uku KAMAL ya sami LABEEBAH
Dan yana kusantarta sai ciwo yaxo mata
Shikuma bayasan hakan

Ayaune yayi waya da wani abokinsa jauhar cikakken likitane wanda yake aiki a asibitin shi KAMAL 'din
Yace mai gasu akan hanya
KAMAL Yace toh ina gida
Bayan ya gama wayanne yake gayama LABEEBAH xuwan abokin nashi da Matarsa
Tace toh tashi katayani aiki kafin Su iso
Hakako akayi ya tayata aikin suka gama sukayi wanka dare dan haka sukeyi
Sai dai daqar KAMAL yake samun kansa idan yana shafa mata mai
Sai tayi da gaske take samun kanta

Bayan sun kintsa kan sune sai ga jauhar da matarsa Amal
LABEEBAH tayi murna da ganinta Sosai duk da yaune farkwan ha'duwarsu
Bayan sunci sunsha
LABEEBAH tajata bet room wai suyi hira

Amal ta girmi LABEEBAH da kusan shekara shidda
Ta kalli LABEEBAH dakyau Tace gaki kyakkyawa kinyi tako ta ina mijinki na sanki Amma kina neman illata rayuwarki
LABEEBAH Tace nayi lefi ko
Tace Wlhi shekaran jiya inajin mijinki KAMAL yana waya da Jauhar yana gaya mishi yana da matsala.
Yace tame
Yace ke raguwace yayinda shi ya kasance mabuqaci. Gashi Kinqi bashi ha'din kai Sam yanda yakeso
Yana ganin xai qara Aure......

LABEEBAH tatashi hannu dafe da qirji Tace Aure
Amal Tace Wlhi Wlhi Allah kenan abinda Naji yana cema Jauhar kenan

Kalleni dakyau LABEEBAH ni Amal na amsa sunan mace dan ba namijin daxai kalleni Yace bankai inda yakesan mace takai ba

Na kasance mace me qarancin sha'awa
Yayinda Mijina Jauhar ya kasance cikakken mabuqaci
Kinsan Allah dake namiji munafukine sai ji nayi an 'daura Auran Sa da wata mace

Sai da naxo ina sauke masa maseefa cikin kuka sai asannan yake cemin wai shi yayi Auranne danni raguwace bani da juriya Sam
Shi kuma baxai iya jure hakan bah
Karki manta watana shidda da Aurena dashi yayimin kishiya akan sex waini raguwace
Ina ji ina gani aka kawomin ita har yanxu muna tare juna

Kinga banbancin Jauhar da mijinki KAMAL 'dayane
Shi KAMAL Yace Sam yana MASEEFAR SONKI kuma bai shirya ha'daki da kowacce mace a rayuwar Auranku bah
Saidai yanxu yanajin Gaskiya xaiqara Aure dan ku6utar da kansa daga fa'dawa xina
Inajinsu Suna tattaunawa
Nayi kamar bansan me suke fa'da. Shine Nace dan Allah ya kawoni inganki
Naci sa'a yayarda
Naji da'din hakan kinga kiyima kanki wiyamullalli kirufama kanki asiri da kishiya dan ba da'dine da itaba Wlhi kixage dantse Ki janyo hankalin mijinki Ki daure koxaki mutu kidinga ba mijin hakkinsa
Dan nasan KAMAL tsaf nayi aiki dashi a asibiti nasan Waye shi idan ya furta abu toko saiya aikata shi
